MATSAYIN HABAICI A ZANTUTTUKAN HIKIMAR HAUSA

By

AZIMA MANSUR AHMAD B.A COMINED (B.U.K. 1999)
MA/ARTS/55819/2005 - 06
MA/ARTS/9662/2009 - 10

A THESIS SUBMITTED TO THE POSTGRADUATE SCHOOL, AHMADU BELLO UNIVERSITY, ZARIA

IN PARTIAL FULFILMENT FOR THE AWARD OF MASTERS OF ARTS IN AFRICAN LITERATURE (HAUSA)

DEPARTMENT OF AFRICAN LANGUAGES AND CULTURES, AHMADU BELLO UNIVERSITY, ZARIA.

AUGUST, 2011

DECLARATION

I declare that the work in the thesis entitled "MATSAYIN HABAICI A ZANTUTTUKAN HIKIMAR HAUSA" has been performed by me in the Department of African Languages and Cultures under the supervision of Dr. Magaji Yakawada Tsoho and Dr. Muhammad Lawal Amin. The information derived from the literature has been duly acknowledged in the text and a list of references provided. No part of this thesis was previously presented for another degree or diploma at any University.

Name of Student	**Signature**	**Date**

CERTIFICATION

This dissertation entitled "MATSAYIN HABAICI A ZANTUTTUKAN HIKIMAR HAUSA" by Azima Mansur Ahmad meets the regulations governing the award of the degree of Master of Arts of Ahmadu Bello University, Zaria and is approved for its contribution to knowledge and literary presentation.

_____ _____

Dr. Magaji Yakawada Tsoho — Date

Chairman, Supervisory Committee

_____ _____

Dr. Muhammad Lawal Amin — Date

Member, Supervisory Committee

_____ _____

Dr. Muhammad Lawal Amin — Date

Head of Department

_____ _____

Prof. A. A. Joshua — Date

Dean, Postgraduate School

SADAUKARWA

Na sadaukar da wannan aiki ga mahaifana Alhaji Mansur Ahmad da Hajiya Zinaru Ahmad.

GODIYA

Dukkan godiya da yabo sun tabbata ga Allah mai kowa mai komai, tsira da aminci su qara tabbata ga Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa da dukkan mabiya har zuwa tashin kiyama.

Ina mai matuqar farin ciki da miqa godiyata ga malamaina Dr. Magaji Yakawada Tsoho da Dr. Muhammad Lawal Amin da Dr. Ahmad Magaji da Malam Bello Alhassan da Dr. Isah Suleiman da Malama Rabi Garba da Dr. Abdullahi Balarabe da Malam Muhammad Tahir da duk sauran malaman da ke Sashen Harsuna da Al'adun Afirka na Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. Allah ya yi musu tukuici da gidan Aljanna.

Haka kuma wajibi ne in miqa godiya ta musamman ga maigidana Malam Isa Musa Gumel, da aminiyata Malama Habiba Yahya Alfadarai da Abdulqadir Ali Ahmad Kabara da duk waxanda suka ba ni gudummawa wajen gudanar da wannan aiki. Allah ya saka musu da alheri.

Ina kuma miqa godiyata ga duk wani wanda ya ba da gudunmawa wajen kammaluwar wannan aiki.

ABSTRACT

The work examines the existence and various manifestations of innuendo (Habaici) in Hausa wise sayings. It also examines its various roles as a genre in Hausa oral literature. Consequently, it is observed that the Hausa's use and exchange innuendoes in most parts of their lives that permeates communications, as well as in poetry, prose and drama. The work further elaborate on the relationship between innuendo and its counterparts like proverbs, epithets, etc. A cursory look on its stylistics pattern was also made.

TSAKURE

Wannan aiki ya yi nazarin Habaici a matsayinsa na wani vangare na zantuttukan hikimar Hausa. Habaici abu ne mai matuqar mihimmanci ga rayuwar Bahaushe wanda ya sanya Bahaushen yin amfani da shi a kusan dukkan vangarori na rayuwarsa da suka haxa da waqa da zube da wasan kwaikwayo da sauransu. Aikin bai tsaya a nan ba sai da ya faxaxa kan irin dangantakar da ke tsakanin habaici da sauran zantuttukan hikima na Hausa kamar su karin magana da kirari da sauransu. A qarshe kuma aikin ya yi tsokaci a kan irin salon da ake amfani da shi a wajen yin Habaici.

ABUBUWAN DA KE CIKI

Take		i
Declaration		ii
Amincewa		iii
Sadaukarwa		iv
Godiya		v
Abstract		vi
Tsakure		vii
Abubuwan da ciki		viii
	BABI NA XAYA: SHIMFIXA	
1.0	Gabatarwa	1
1.1	Matsalolin Bincike	2
1.2	Iyakar Bincike	3
1.3	Dalilin Bincike	3
1.4	Hanyoyin Tattara Bayanai	4
1.5	Kammalawa	7
	BABI NA BIYU: WAIWAYEN AYYUKAN DA SUKA GABATA	
2.0	Gabatarwa	8
2.1	Kundayen Bincike	8
2.2	Bugaggun Littafai	14
2.3	Maqalu da Mujallu da Sauran Takardun Bayanai	16
2.4	Kammalawa	19
	BABI NA UKU: MUHALLAN HABAICI	
3.0	Gabatarwa	20
3.1	Bayani a kan Habaici	21
3.2	Ma’anar Habaici	24

3.3 Muhallan Habaici 24
3.3.1 Habaici a Zube 25
3.3.1.1 Habaici a Karin Magana 25
3.3.1.2 Habaici a Take 29
3.3.1.3 Habaici a Kirari 30
3.3.1.4 Habaici a Zambo 31
3.3.2 Habaici a Waqa 36
3.3.3 Habaici a Wasan Kwaikwayo 40
3.4 Habaici a Zantuttukan Yau da Kullum 40
3.5 Kammalawa 42

BABI NA HUXU: JIGOGI DA AMFANIN HABAICI

4.0 Gabatarwa 43
4.1 Matsayin Habaici ga Al'ummar Hausawa 43
4.1.1 Habaici Tsakanin maza 46
4.1.2 Habaici Tsakanin mata 47
4.2 Jigogin Habaici 49
4.2.1 Habaici don Kushe 52
4.2.2 Habaici don Faxakarwa 52
4.2.3 Habaici don Wa'azi 53
4.3 Amfanin Habaici 58
4.3.1 Burgewar Harshe 58
4.3.2 Habaici kan taimaka wajen taqaita magana 60
4.3.3 Gargaxi 61
4.3.4 Huce takaici 62
4.4 Kamalawa 66

BABI NA BIYAR: SALO A HABAICI

5.0 Gabatarwa 67

5.1 Ma'anar Salo da Tubalansa 67

5.2 Salo a Habaici 68

5.2.1 Salon Tsari a Habaici 69

5.2.1.1 Habaici mai Qaramar Jimla 69

5.2.1.2 Habaici mai Labari 69

5.2.1.3 Habaici mai "In ji" 70

5.2.1.4 Habaici mai Vangare Biyu 70

5.2.1.5 Habaici mai Tambaya da Amsa 71

5.2.1.6 Sababbin Habaici 71

5.2.2 Salon Sarrafa Harshe a Habaici 71

5.2.2.1 Kamantawa 72

5.2.2.2 Abuntawa 72

5.2.2.3 Mutuntawa 73

5.2.2.4 Dabbantarwa 74

5.2.2.5 Rayarwa 75

5.3 Habaicin Mata 75

5.4 Sigogin Habaici 84

5.5 Kammalawa 88

BABI NA SHIDA: NAXEWA

6.0 Gabatarwa 90

6.1 Abubuwan da Bincike ya Gano 91

6.2 Shawarwari 91

6.3 Kammalawa 93

MANAZARTA 94

BABI NA XAYA: SHIMFIXA

1.0 Gabatarwa

Kowace al'umma ta duniya tana da hanyoyinta na zantuttukan hikima da take amfani da su a cikin harshenta don nuna gwaninta da kinaya da dabara da vad-da-bami a cikin harshen yayin da buqatar hakan ta samu.

Harshen Hausa cike yake da zantuttukan hikima na wanda za a iya cewa ana yin su ne ba kurum don nuna qwarewa da basirar sarrafa harshe ba, ana kuma yin amfani da su domin isar da saqo cikin nishaxi.

Bugu da qari duk wata qirqira ta zantuttukan hikima walau sabuwa ko tsohuwa duk ilahirin ma'anar da ta qunsa tana cikin harshen da wannan al'umma ke amfani da shi kamar yadda yake a harshen Hausa.

Ke nan harshen Hausa cike yake da zantuttukan hikima masu qayatarwa, kamar su habaici da karin magana da kirari da zambo da take da makamantansu, kamar yadda wannan bincike ya yi nazarin habaici a zantuttukan hikima na Hausawa.

Baya ga ado da bunqasa harshe da habaici ke yi a harshen Hausa babban abin dubawa shi ne irin saqon da yake isarwa ga al'umma da salailan da yake da shi da kuma irin yadda ake amfani da shi wajen gargaxi da huce haushi da mayar da martani da wajen faxakarwa, wani lokaci ma har da koyar da wasu abubuwa da suka shafi halin rayuwar yau da kullum.

1.1 Maqasudin Bincike

Habaici wani nau'i ne na zancen hikima da ake amfani da shi a nusar da mutum a fakaice. Yawanci habaici yakan qunshi kwatanta wasu abubuwa da nufin nuna gazawa ko raini ko mayar da martani ga wanda aka yi wa shi (Umar, 1980:24).

A wannan bincike an yi nazarin habaici a zantuttukan hikima na Hausawa, dangane da haka akwai matsaloli da aka ci karo da su kamar haka:-

- Guntayen zantuttukan hikima na Hausawa sun haxa da karin-magana da take da kirari da zambo da gatse da baqar-magana da shaguve da habaici da sauransu. A nan tambayar ita ce, yaya kowane xaya daga cikin su yake?
- Shin akwai wani abu habaici?
- Yaya salailansa su ke?
- Wane irin muhimmanci yake da shi ga al'umar Hausawa.
- Sa'annan shin habaicin na taka rawa dangane da abubuwan da suka shafi rayuwar Hausawa?
- Idan akwai, waxanne abubuwa ne?

1.2 Iyakar Bincike

Wannan bincike ya taqaita ne a wani vangare na cikin guntattakin zantuttukan hikima na Hausawa.

An yi nazarin habaicin da kuma zantuttukan hikima masu alaqa da shi kamar su karin magana da take da kirari da zambo da sauransu.

Dangane da habaicin kuma an duba ma'anarsa da salailansa da saqonnin da yake xauke da su zuwa ga al'umma da makamantansu.

1.3 Dalilan Bincike

Duk da cewa masana da dama sun yi tsokaci game da zantuttukan hikima na Hausawa, wannan bincike ya yi sharhi a kan habaici daga cikin waxannan zantuttuka domin yana da matuqar muhimmanci.

Gudanar da bincike a kan wannan batu ya taimaka matuqa wajen samar da bayanai ga xalibai da dukkan masu nazari a kan abin da ya shafi wannan fanni.

Binciken ya nemi ya gano:

- Idan akwai habaici – don me aka gina shi, yaya tsarinsa yake?
- Su wa suka fi amfani da shi? Don me?
- Sannan wane irin saqo yake xauke da shi?

1.4 Hanyoyin Tattara Bayanai

Dangane da binciken da aka gudanar an bi hanyoyi da dama wajen tattara bayanai da suka haxa da:

i) Xakunan Karatu

Dangane da wannan aiki an ziyarci xakunan karatu kamar haka:

- Babban xakin karatu na Kashim Ibrahim da ke Jami'ar Ahmadu Bello ta Zariya.
- Xakin karatu na Sashen Harsunan Nijeriya da Afrika da ke Jami'ar Ahmadu Bello ta Zariya.
- Babban xakin karatu na Jami'ar Bayero da ke Kano.
- Xakin karatu na Sashen Harsunan Nijeriya da ke Jami'ar Bayero ta Kano.
- Gidan Adana Taskokin Bayanai na Mambayya da ke Kano.
- Xakin karatu na makarantar gaba da sakandare ta Bammali da ke Zariya.

Dangane da ziyarce-ziyarcen xakunan karatu, wannan ya bada dama an karanta littattafai daban-daban waxanda suka haxa da na zube da na wasan kwaikwayo don samun habaice-habaicen da Hausawa ke amfani da su yau da kullum.

An kuma nazarci ayyuka da dama da suke da nasaba da wannan batu har da rubuce-rubucen adabi domin a gwada muhimmancinsa domin masana sun ce adabi matsokaci ne na al'umma.

ii) Ganawa

Wajen gudanar da wannan bincike an gana da rukunin mata daban-daban har uku, daga ciki akwai mata matasa da matan aure da kuma dattawa.

Daga cikinsu akwai:

Mata Matasa:

- Talatu Muhammad
- Binta Xan'auta
- Fati Usman
- Bilki Inuwa

Matan Aure

- Tasidi Yahaya
- Bilkisu Usman
- Maimuna Ado
- Hauwa Garba

Mata Dattijai

- Hajiya Inno
- Uwar Marayu
- Hadiza Yusha'u
- Rabi Mairiga

Ga yadda tsarinsu yake:

Lamba	Suna	Shekara	Gari	Yanayi
1	Talatu Muhammad	16	Kano	Budurwa
2	Binta Xan'Auta	18	Zariya	Budurwa
3	Fati Usman	17	Sakkwato	Budurwa
4	Bilki Inuwa	19	Katsina	Budurwa
5	Tasidi Yahaya	32	Kano	Matar aure
6	Bilkisu Usman	36	Zariya	Matar aure
7	Maimuna Ado	34	Sakkwato	Matar aure
8	Hauwa Garba	33	Katsina	Matar aure
9	Hajiya Inno	60	Kano	Gyatuma
10	Uwar Marayu	55	Zariya	Gyatuma
11	Hadiza Yusha'u	62	Sakkwato	Gyatuma
12	Rabi Mairiga	61	Katsina	Gyatuma

iii) Xakunan Fasahar Baka

An saurari waqoqin baka nan ma don jin irin habaice-habaicen da mata suke yi wa 'yan'uwansu mata ko kuma wani rukuni na jama'a. Daga ciki akwai:

- Waqar Coge ta Barmani Coge, da kuma ta
- Hauwa Mai'amada

1.5 Kammalawa

Bayanan da suka gabata sun share fage ne a kan inda wannan bincike ya dosa tare da muhimmancinsa da kuma inda ya tuqe, ma'ana inda binciken ya tsaya.

An fitar da matsalolin bincike waxanda suka bada damar aka yi tambayoyi da kawo amsoshi da za su kawar da matsalolin.

Sa'annan an kawo manufa da iyaka tare da hanyoyin da aka bi wajen tattara dukkan bayanan wannan bincike.

BABI NA BIYU: WAIWAYEN AYYUKAN DA SUKA GABATA

2.0 Gabatarwa

Hausawa kan ce “da na gaba ake gane zurfin ruwa, ko da kuwa na gaban wada ne”. An sami ra’ayoyi da dama game da habaici, wanda ya nuna cewa habaici wani muhimmin rukuni ne a adabin Hausa shi ya sa Hausawa sukan ce “maso habaici maso faxa, wanda ya rama da shi ake”.

Wannan babi tsokaci ya yi dangane da ra’ayoyin jama’a daban-daban a kan habaici inda wani ra’ayin ke ganin habaici a matsayin magana ce ta takalar fitina, wani kuma ke ganin matsoraci ke yin amfani da shi, wani kuwa ta’allaqa habaici ya yi wajen mata. Saboda haka an xauki mabambanta ra’ayoyin tare da fayyace masu ra’ayin ko kuma vangarorin da yadda ake amfani da shi.

2.1 Kundayen Bincike

Kundayen bincike da dama na manazarta sun yi magana a kan habaici a inda suka kalle shi ta fuska daban-daban. Daga cikin waxanda aka yi nazari wajen gabatar da wannan bincike sun haxa da Ibrahim, (1995) da Sanyinna (2002) da Umaru, (1986) da Safara’u, (1994) da Magaji, (1980) da sauransu.

Ibrahim (1995) cewa ya yi habaici wasu maganganu ne da ake faxa a fakaice don vata wa wani ko wata rai ba tare da bayyana mutum ba. Ya qara da cewa habaici idan ba mutum ya san kan zance ba, ba kasafai ake gane

wanda ake yin habaicin domin sa ba don kuwa ana laqaba shi ne da wani abu da ya faru kan wani mutum da ya aikata abin da yake ba mai kyau ba.

Marubucin ya kalli habaicin ne a waqe inda ya duba shi a matsayin wani jigo na dangantaka tsakanin waqar baka da rubutatta, sai dai shi wannan bincike ya fi bada qarfi wajen shi kansa habaicin ne a aikace.

Shi kuwa Sanyinna (2002) a kundin bincikensa da ya gabatar, ya nuna cewa habaici ya qunshi maganganu ne amma fa ba na daxi ba sai dai ba sukan tafi ba ne kai tsaye don a fakaice ake bada su.

Bayan da marubucin ya qwanqwance kuma ya kalli habaicin kamar haka:

1- Cewa habaici wata hanya ce da ake bi a yi amfani da kalmomi don a tsokani ko a muzanta ko a ba wani haushi a fakaice saboda wasu dalilai na rayuwa da ke gudana a tsakanin mutane na yau da kullum.

2- Haka ma ana iya cewa “habaici maganganu ne na hikima da ake yi don a sosa wa wani rai cikin hikima da dabaru irin na Bahaushe waxanda yakan shirya don mayar da martani ko huce haushi”.

3- Har wa yau ana iya kallon habaici a matsayin “wasu kalmomi ne masu sha’awa a cikin zance kuma masu ban dariya ga mai saurare, amma kuma masu sa ban takaici da sanya baqin ciki ga wanda aka nufa da su”.

4- Kuma idan an kalli habaici da kyau, ana iya cewa “magana ce cikin magana, amma fa mai qunshiyar wani saqo na musamman zuwa ga wani ko wata. Ana iya fahimtar wanda ake nufi da saqon a wasu lokutta sai dai saqon ba mai daxi ba ne ga wanda aka nufa da shi”.

5- Kuma ana iya cewa “habaici rigar fitina ne ake xinkawa ana neman mai son ya sa a wuyansa, duk da kasancewar an san wanda aka xinka rigar saboda shi, idan ya sa ta dace da shi, idan bai sa ba an qware shi”.

Marubucin bai tsaya a nan ba sai ya ci gaba da kawo wasu zantuttukan hikima da suka yi kama da habaici kamar karin magana da sauransu, ya kuma yi qoqarin fayyace ma’anarsu a fili, sai dai binciken nasa ya sha bamban da wannan domin shi ya kalli habaicin ne a waqa kurum amma shi wannan binciken ya kalli shi a kusan kowane vangare na adabi kamar zube da wasan kwaikwayo da sauransu.

Umaru, (1986) ya gabatar da bincike a kan zantuttukan hikima na Hausa, inda ya bayyana habaici da cewa gajere ne kuma taqaitacce ya kuma nuna cewa dukkan habaici karin magana ne sai dai ba dukkan karin magana ne habaici ba. Dangane da tsarin habaici ya qunshi kalmomi waxanda aka shirya don su daxa taimakawa wajen cimma burin da ake so. A yawancin lokutta, akan yi habaici ne don yin shaguve ko hannunka mai-sanda a kan wani abu.

Marubucin ya yi tsokaci a kan dangantakar da take tsakanin zantuttukan hikima inda ya nuna cewa dukkan su ana yin su ne don nuna qwarewa da basirar sarrafa harshe, wato dai dukkansu ana amfani da su don burgewa da kuma yin wani gargaxi ko nasiha ga jama'a a fakaice. Abin nufi da burgewa dangane da habaici shi ne yadda ake amfani da shi cikin al'umma dangane da halin zaman yau da kullum don yanayin savawa ko husuma, kamar yadda ya nuna.

Wannan yanayi ya zo dai-dai da wannan bincike da aka gabatar domin shi ma wannan binciken ya maida hankali ne wajen gudummawar da shi habaicin yake bayarwa ga al'umma, ta yadda ake amfani da shi wurin gargaxi da nasiha a fakaice ko faxakarwa ta fuskar addini ko musgunawa duk dai a halin rayuwa ta yau da kullum. Misali in duniya ta shimfixa maka tabarma, zauna a gefe.

Marubucin bai tsaya a nan ba, sai ya bayyana vangarorin da suka fi amfani da habaici ya kuma qara da cewa mun riga mun san cewa kowanne sashi na adabin bakan Hausawa wanda yake da dangantaka da sarrafa harshe ta hanyar azanci da hikima da basira akwai waxansu qungiyoyin jama'a da aka fi dangantawa da yin amfani da irin wannan vangare. Bugu da qari, ana kuma yin la'akari da dalilan da suka sa ake ganin su waxannan qungiyar jama'ar sun fi amfani da wannan sashe na hikimar sarrafa harshe. Ya nuna cewa waxanda suka fi amfani da habaici su ne, malaman addini da gidajen watsa labarai da kuma masu hikima.

A vangaren malaman addini ba wai yana magana a kan wani addini ba ne, illa addinin Musulunci da kuma irin hikimar da take qunshe a cikinsa, wanda yake ganin ya sa duk wanda ya naqalci wannan ilimi za a taras da hikima da basira cikin maganarsa.

Masu hikima kuwa ya nuna cewa duk inda aka ambaci kalmar hikima, abin da zai fara zuwa a zuciyar mai sauraro shi ne basira ko dabara ko azanci. To dukkan waxannan an fi danganta samun su ga mai ilimi domin kuwa, shi kansa mai hikima da ilimi yake wadatuwa. Ya nuna cewa wannan kashi ya kamata ya zo a qarqashin kashi na farko don muhimmancinsa to amma ganin cewa yawancin Hausawa da zantuttukansu suke cike da hikima da basira ba su fiye iqirarin cewa su malamai ba ne sai dai sukan danganta maganganunsu da cewa “malamai kan ce” shi ya sa wannan kashi ya sami zaman kansa.

Marubucin ya qara da cewa gidajen watsa labarai wani sashe ne da ke amfani da zantuttukan hikima wajen wayar da faxakar da jama’a, sukan kuma taimaka wajen isar da saqon gwamnati ta hanyar amfani da habaici don sadarwa ga jama’a.

Vangaren gidajen Rediyo kuwa marubucin ya bada misalansa da wani shiri na musamman da gidan rediyon tarayya na Ikko kan gabatar a wancan lokaci mai suna “*The Words of Our Elders are the Words of Wisdom*”, wanda za a iya fassara shi da “masu hikima sun ce” wanda a wannan shiri, akan tsara zantuttukan hikima ne waxanda duk wanda ya ji su zai san akwai

basira da azanci a tare da su kuma akwai saqon da suke isarwa ga jama'a, amma a fakaice. Wato sai mai hankali da natsuwa zai iya fahimtar abin da ake nufi. Haka kuma akwai shirin "In kunne ya ji" wanda gidajen rediyon Kano da Kaduna ke yi don yin hannunka-mai-sanda ga jama'a.

Ya qara da cewa gidajen jaridu ma ba a bar su a baya ba wajen yin amfani da irin wannan zance na hikima domin suna taimaka wa gwamnati ta hanyar yin gargaxi da faxakarwa ga jama'a don kyautata xabi'unsu.

Kusan dukkan vangarorin da marubucin ya zana, wannan bincike ya yi amanna cewa suna cikin vangarorin da ake gudanar da habaici, amma binciken ya sha bamban da wannan domin shi wannan ya fi bai wa habaicin qarfi a aikace. Shi kuma ya xauki habaicin ne a zantuttukan hikima kawai musamman vangaren Karin Magana. In muka duba za mu ga cewa wasu habaice-habaicen kuma ana gudanar da su tsakanin mata, za mu iya yin la'akari da abin da Safara'u (1994) ta gabatar a cikin bincikenta na kundin digiri na farko inda ta xan tava ire-iren habaicin mata.

Marubuciyar ta ce habaicin mata shi ne habaicin da da zaran an yi shi za a san cewa mace ke ma 'yar'uwar zamanta ko wata matar daban kamar maqwabciya, ko kuma wanda daga ji za ka san cewa mace ce ke ma maigida. Haka kuma akwai wanda daga an ji za a san budurwa ce ke ma saurayi ko wani namiji.

Dalilin ko da ya sa aka kira wannan habaici na mata shi ne, don an fi jin irin su daga bakin matan amma ba dole ne sai ga matan kawai ba. Domin

takan iya yiwuwa a wasu lokutta a ji maza suna amfani da su ko suna yin su, kuma irin wannan habaici an fi amfani da jinsi ne na mata.

Shi kuwa Magaji, (1980:60) duk da cewa ya gabatar da bincikensa a kan qassu zurmi ne, ya bayyana habaici da cewa shi ne yi da mutum da magana a voye. Akan faxi wasu kamannu ko kuma hali na mutum yadda daga ji za a fahimci ko da wa ake yi.

Wannan bayani yana nuni da cewa shi habaici ana yin sa ne cikin hikima kasancewar ba fito da maganar ake yi kai tsaye ba.

2.2 BUGAGGUN LITTATTAFAI

An sami bayanan habaici a bugaggun littattafai da maqalu da mujallu da takardun bayanai da dama.

Daga cikinsu akwai Xangambo (1982) da Bargery (1934) da Gusau (1980) da Umar (1980) da Zarruq da abokan talifinsa (1982).

Kusan dukkan waxannan masana sun yi magana ne kan ainihin ma'anar habaicin, don haka sun yi tarayya kan abu guda, domin sun kalli habaicin ta fuskar ma'ana.

Xangambo, (1984) ya fito da ma'anar habaici qarara, inda ya nuna cewa habaici, magana ce mai voyayyiyar manufa. Akan yi magana da niyyar nufin wani abu ga wanda aka yi maganar dominsa. To, amma shi habaici, idan ba mutum ya san kan zance ba, ba kasafai ake gane wanda aka yi habaicin dominsa ba. Wannan ya zo daidai da Gusau (1980) domin shi ma

ya nuna cewa maganganu ne da ake faxar su a fakaice wanda ya zo daidai da rashin fito da su (maganganun) qarara. Ya ci gaba da cewa ana yin habaici ne don vata wa mutum rai wanda ya zo daidai da yadda Umar (1980) ya kalli abin, domin shi kuma ya nuna cewa habaici kan qunshi kwatanta wasu abubuwa da nufin nuna gazawa ko raini ko mayar da martani ga wanda aka yi wa shi, wanda dukkanin waxannan alamu na vata wa mutum rai ne.

Bargery (1934:431) shi kuma ya bayar da tasa ma'anar inda ya nuna cewa halayyar mutum ake masa shaguve da ita a gabansa wanda ya qara da cewa habaici na iya zama jirwaye da kamar wanka ko ma shaguve kai tsaye. Har ila yau, Bargery ya qara bada ma'anar shaguve da cewa shi ma habaici ne domin ya ce yi ne da mutum a gabansa ba tare da ambatar sunansa ba. Wanda ya zo daidai da bayanin Zarruq (1986:47) da abokin talifinsa, suka bayar inda suka ce shi habaicin shaguve ne ma kai tsaye,

Sun kuma qara da cewa habaici yi ne da mutum a kaikaice. Habaici ya fi yawa inda kishi yake ko qyashi. Galibi mutane suna xauka habaici salon mata ne, dalili kuwa shi ne a tsakanin mata kishi da ganin qyashi suka fi yawa.

Kusan dukkan bayanan da suka gabata a kan ma'anar habaici suna nuni ne da cewa habaici ana yin sa ne cikin hikima, kasancewar ba fito da maganar ake yi kai tsaye ba. Ma'ana akan yi ta ne cikin hikima ba tare da an kira suna ba, amma mafi yawan lokaci kalmomin da aka yi amfani da su sukan sa mutum ya gane da wanda ake idan dai ya san shi. Habaici ba ya

qunsar abu mai kyau na wanda ake yi wa, yawanci wasu abubuwa ne na nuna gazawa ko raini ko mayar da martani ga wanda aka yi wa shi.

2.3 MAQALU DA MUJALLU DA SAURAN TAKARDU

Maqalu da mujallu da sauran takardun bayani na masana da manazarta daban-daban, sun yi kyakkyawan duba game da habaici. Daga cikinsu akwai Dunfawa, (2005) da Bichi, (1997) da Muhata,. da Bichi, (1995). Kowanne daga cikin waxannan masana ya tofa albarkacin bakinsa a kan habaici, ga abinda suka ce:

Dunfawa, (2005) kallon habaici ya yi ta vangaren faxar aibin mutum a fakaice tare da sanar da shi cewa ana sane da wani mugun aiki da yake yi wani lokaci har akan nuna masa yadda zai yi ya gyara.

Binciken nasa ya yi kama da wannan domin ya yi qoqarin bayyana matsayin habaici ga halayyar xan'Adam, wanda shi ma wannan bincike ya shafi matsayin habaicin ga xan'Adam xin ne.

Marubucin ya nuna cewa habaici abu ne halittacce ga halayyar xan'Adam wanda ke cikin jininsa, kasancewar Allah ya halicci mutum mai tsananin son kai wanda ya haifar masa da buqatar kowa ya so abin da yake so ko kuma ya qi abin da yake qi, wanda savanin haka abin da zai fara yi shi ne nuna qin haka ta fuskar amfani da baiwar da Allah ya yi masa ta magana don kushe wanda ko waxanda suka sava ma nufinsa, shi ne ya aibanta wancan nufin da ba nasa ba (varo-varo ko a fakaice), wajen yin haka sai

habaici ya samu, kowane matsayi na rayuwa mutum yake, yana iya amfani da habaici don kushe abokin hamayyarsa.

Binciken na Dunfawa (2005) ya xan sha bamban da wannan domin shi kusan ya kalli habaicin ne ta fuskar addini, wanda shi kuma wannan bincike ya xauki vangaren halayar zamantakewa ta xan'Adam tsakanin al'umma, musamman yadda suke amfani da habaicin a aikace.

Bichi, (1997) ya gabatar da takarda mai taken "*Current Trends and Issues in Hausa Proverbs"* a takardar tasa ya gabatar da irin rawar da karin magana ke takawa a harkokin al'ummar Bahaushe na yau da kullum wanda ya haxa da amfanin karin magana wajen wayar wa da mutane kai a kan abubuwan da suka shafi rayuwa da ilmantarwa ta vangaren ilimin zaman duniya da na addini da vangaren siyasa, uwa uba kuma kai har da vangaren addini.

Kasancewar karin magana da habaici Xanjuma ne da Xanjummai idan muka yi kyakkyawan duba za mu ga cewa binciken nasa ya yi kama da wannan domin ya tavo karin magana a vangaren addini.

Haka zalika in aka yi duba ga wannan binciken za a ga cewa shi ma ya zaqulo irin amfanin da habaici ke yi wajen faxakarwa ta fuskar addini, wannan ya tabbatar da cewa binciken biyu na da alaqa da juna.

Haka kuma binciken nasa ya sake yin duba inda ya bayyana mana cewa karin magana na da matuqar muhimmanci wajen sadarwa tsakanin al'ummar Hausawa, haka kuma wannan binciken ya nuna irin yadda ake

amfani da habaici wajen sadarwa ko isar da saqo tsakanin al'ummar Hausawa.

Mahuta, a takardarsa da ya gabatar mai taken matsayin mata a kare-karen magana na Hausa "*the Status of Women in Hausa Proverbs*" ya tava vangarori daban-daban wanda suka shafi mata, domin ita kanta takardar an gabatar da ita ne a kan matan ko kuma matsayinsu a karin magana ta Hausa, haka wannan binciken ya tava bayani a kan salon habaicin mata.

Bayan kyakkyawan duba za a qwanqwance cewa da nasa binciken da wannan dukkansu an gabatar da su ne a kan al'ummar Hausawa kuma vangaren abin da ya shafi zantuttukan hikima na Hausa, wancan karin magana wannan kuma habaici. Ta vangaren jinsi za a ga cewa nasa mata ya tava wanda wannan ma ya tava su. Haka ta vangaren gundarin batun kowanne ya tava zantuttukan hikima ne na Hausawa.

Bichi, (1995) a wata takardar da ya gabatar "*Hausa Folkgenres*" ya tava tsatsuniyoyi da waqoqin yara, bai tsaya a nan ba sai ya wuce kan karin Magana, inda ya nuna muhimmancinsu a matsayin wani babban kashi na adabin Hausa. Ya bayyana cewa harshen Hausa na cike da karin magana masu qayatarwa wanda hakan bai hana qirqirar wasu ba.

Ya sake jaddada muhimmancinsu wajen sadarwa sannan ya fito da cewa suna koya mana xabi'a mai kyau domin magabata kan yi amfani da su wajen gargaxi ko koya wa yara xabi'a mai kyau.

Binciken ya yi kama da wannan, domin yadda ya nuna ana amfani da karin magana don gargaxi ko faxakarwa, wannan binciken ma ya fito da yadda ake amfani da habaici wajen gargaxi ko faxakarwa ta fuskar addini qarara.

2.4 KAMMALAWA

Waxannan bayanai sun qunshi tsokaci ne na masana daban-daban da suka yi kan ma'anar habaici da kuma yadda suke kallonsa.

Bai tsaya ga nan ba domin akwai hasashen mai binciken game da ra'ayoyin masana, inda ta fitar da inda masanan ke da alaqa da juna ko suka sha bamban dangane da irin rubuce-rubucen da suka yi a kan habaici ko kuma zantuttuka masu alaqa da shi.

Dangane da haka ko kuma game da waxannan nazarce-nazarce, habaici na nufin yi da mutum ko kuma faxa masa wata magana marar daxi a kaikace. Har ila yau kuma habaici ya kasu kashi daban-daban musamman ta hanyar da ake bi wajen amfani da shi.

BABI NA UKU: MUHALLIN HABAICI

3.0 Gabatarwa

Wannan babi yana qunshe da bayani a kan ma'anar habaici da muhallansa, wato inda habaici yake fitowa, da yadda kuma tsarinsa yake. Har ila yau za a duba dangantakarsa da sauran zantuttukan hikima na Bahaushe kamar su kirari da karin magana da take da sauransu.

Binciken bai yi qasa a gwiwa ba sai da ya kalli habaicin a waqe ko a zube ko a wasance da ma a cikin zantuttuka na yau da kullum.

3.1 Bayani a Kan Habaici

Kamar yadda bayani ya gabata, habaici shi ne zagin wani mutum ko faxa masa wata magana marar daxi a fakaice, abin da wasu kan kira gugar zana ko riga-ba-wuya. Habaici magana ce mai zafi wadda akan yi ta a lulluve. Sau da yawa wanda aka yi wa habaicin yakan gane da shi ake yi, har ma in ya ga dama ya rama. Habaici zance ne da ake lulluva wa mayafi, ba a bar shi tsirara ba, don ba a fito fili an ambaci sunan wani ko wata ko a ce sun yi wani abu ba, don saboda dabara da hattara ta xan'Adam, amma da zarar an yi sun san da su ake.

Idan aka lura, an fi samun habaici ta fuskar kishi. Shi kuma kishi ko rashin jituwa tsakanin kishiyoyi kan haifar da yin habaici a tsakaninsu maimakon tunkarar juna gaba-gaxi. Hikimar mata ta iya zance ta sanya su yawaita yin habaici a junan su don vata wa wata ko kuma don maida martani.

Misalin habaici a nan shi ne: "*wata ta dafa ta sayar, wata ta dafa ta zubar"*.

Mace kan yi amfani da wannan in ta fi kishiyarta iya girki kuma mijin da mutanen gida sun fi jin daxin abincinta.

3.2 Ma'anar Habaici

Masana da manazarta adabi sun yi qoqarin bayyana ma'anar habaici ta fuska daban-daban. Ibrahim, (1983) ya ce "Habaici wani jigo ne da makaxan sarauta suke amfani da shi don su bai wa mutane dariya".

Xangambo (1984:42) ya bayyana cewa "Habaici magana ce mai voyayyiyar manufa. Akan yi magana da niyyar nufin wani abu ga wanda aka yi maganar dominsa. To amma, shi habaici idan mutum bai san kan zance ba, ba kasafai ake gane wanda ake yi wa habaicin ba".

Umar (1980:24) cewa ya yi "habaici wani nau'i ne na zancen hikima da ake amfani da shi a yi da mutum a fakaice, yawanci habaici kan qunshi kwatanta wasu abubuwa da nufin nuna gazawa ko raini ko mayar da martani ga wanda aka yi wa shi".

Magaji, (1980:60) ya ce habaici shi ne yi da mutum da magana a voye. Akan faxi wasu kamannu ko kuma hali na mutum yadda daga ji za a fahimci ko da wa ake yi.

Bargery, (1934:431) bayyana habaici ya yi da yi wa mutum shaguve dangane da halayyarsa a gabansa ba tare da ambatar sunansa ba. Hausawa

sukan ce habaici yakan iya zaman jirwaye da kamar wanka ko shaguve ko feshi ko kuturun kinibibi.

Zarruq da wasu (1982:47) cewa suka yi “habaici dai shaguve ne, watau Hausa ce cikin Hausa, galibi a kan abin da ya sosa wa mutum zuciya. Yawancin habaici ana yin sa da nufin ramuwar gayya ne ko maida martini. Maganarsa mai ciwo ce, kuma mai wuyar ramawa kai tsaye. Domin akan san wanda aka nufa da habaicin duk kuwa da ba sunansa aka ambata ba. Saboda haka shi ma idan zai rama ba zai ambaci suna ba”.

Idan muka dubi waxannan ma’anoni daban-daban, muna iya cewa habaici kalmomi ne da ake amfani da su a fakaice. Don muzanta wani ko yi da shi. A wajen yin habaici ba a bayyana wanda ake nufi quru-quru, sai dai akan yi amfani da wasu kalmomin sakayawa kamar wani ko wasu da makamantansu.

Alal misali, idan muka yi la’akari da ma’anar da Xangambo, (1984:42) ya bayar za mu ga lallai habaici magana ce a taqaice don ya nuna ba kasafai ake gane wanda ake yi wa shi ba, in dai ba mutum ya san kan zance ba. Haka kuma ba a fito da maganar qarara sai dai a sakaya, amma fa wanda aka nufa da maganar ya san da shi ake, haka ma waxanda suke da masaniya a kan maganar za su rarrabe da barcin makaho.

Wannan hange na masanin (Xangambo, 1984) ya yi kama ko kuma shige da na Magaji, (1980:60) inda shi ma ya nuna ba wai gadan-gadan ake fidda zancen habaici ba, akan yi da mutum ne da magana a voye, ma’ana,

voyayyiyar manufa ke da maganar ba kai tsaye ba sai dai ya nuna faxar halayya ko wasu kamanni na mutum kan sa a fahimci ko da wa ake yi. Binciken na masanin ya sha bamban da na Xangambo (1984) domin shi ya nuna duk da qarya ta fi yawa a cikin habaici, akwai ‘yar gaskiya wanda shi Xangambo (1984) bai fayyace hakan ba, sai dai shi ma ya nuna, ba kasafai ake gane wanda ake yi wa habaicin ba, wanda ya zo daidai da maganar nan ta Hausawa da suke cewa: “*maso habaici maso faxa, wanda ya tanka ya shi*”.

Domin daga ji an san ba kiran suna mai habaici yake yi ba, ba kuma gadan-gadan yake nufar wanda yake wa habaicin da maganar ba sai dai yakan xan sakaya, amma fa wannan bai hana saqon isa ga wanda ake da shi ba.

Har ila yau binciken Magaji, (1980) ya yi kama da na Bargery, (1934) domin kowannen su ya nuna akan tava vangaren halayya a habaici, wato a faxi wani hali na mutum yayin yi masa habaicin yadda daga an ji za a san da shi ake. Binciken na Bargery, (1934) ya yi kama da na Zarruq da Alhassan (1982) domin nasu binciken ya fito qarara ya nuna habaici yi wa mutum shaguve ne dangane da halayyarsa, yakan iya zama jirwaye da kamar wanka ko feshi ko kuturun kinibibi. Haka zalika su ma sun fito qarara sun nuna habaici shaguve ne, wato Hausa cikin Hausa, amma galibi a kan abin da ya sosa wa mutum zuciya. Sun kuma qara da cewa yawancin habaici ana yin sa

da nufin ramuwar gayya ne ko maida martani, wanda maganar kan zama mai ciwo mai kuma wuyar ramawa kai tsaye.

Wannan bincike ya gano cewa lallai habaici yana iya zama tsokanar faxa tun da magana ce ba ta daxi ba, kuma dole idan an yi ta akwai wanda aka nufa da ita sai dai takan zama mai wuyar ramawa nan take tun da ba kiran suna ake ba sai dai akan ya da magana ne kawai. Game da habaici, Hausawa sun ce wanda aka yi wa ya tanka ya fi wanda ya fara neman faxan, tunda shi mai magana ta farko ya saka mata hijabi, bai bar ta tsirara ba domin bai fito qarara ya ce ga wanda yake yi da shi.

3.3 Muhallan Habaici

Idan aka ce muhalli ana magana ne a kan gida ko gurbi na wani abu, don haka muhallan habaici sun kasance duk wani gurbi da ake samun habaici. Waxannan muhallai sun shafi duk wani vangare ko rukuni da za a iya samun habaici.

Masana sun nuna cewa habaici na iya fitowa ko dai a zube ko a waqe ko a wasan kwaikwayo kai har ma da zantuttukan yau da kullum. Dangane da haka za mu duba waxannan gurabe na habaici.

3.3.1 Habaici a Zube

Xangambo, (1984:9) ya bayyana zube a matsayin duk wata wallafa da ba waqa ba ce ba kuma wasan kwaikwayo ba. ma'ana zance ce da ake yi kara zube ba tare da tsari ko siffa irin na wasan kwaikwayo ba.

Zube wani rukuni ne babba a adabin baka, wanda kuma samun ilimin karatu da rubutu ga Hausawa ya samar da shi a rubuce.

Dangane da Adabin Bahaushe a kan kasa zube gida biyu:

i) Magantaccen Zube.
ii) Rubutaccen Zube

ii) Magantaccen Zube:

Magantaccen zube na cikin rukunin adabin baka na Bahaushe wanda Bahaushe ya samar da ka yake gabatarwa da baki, sannan ya adana su a ka.

Daga cikinsu akwai karin magana da kirari da zambo da take.

3.3.1:1 Habaici a Karin Magana

Manazarta sun yi ta qoqari wajen fito da ma'anoni waxanda suke ganin su ne haqiqanin ma'anar ko dai habaici ko kuma karin magana, inda za a iya ganin inda kowanne ya fuskanta kamar misali Zarruq da sauransu (1986:45) suka yi qoqarin bayyana karin magana a matsayin "Gajeren zance wanda yake qunshe da hikima". Duk da cewar za a iya ganin rashin cikakkiyar tantancewa game da wannan ma'ana domin kuwa duk wani zancen hikima wanda ya taqaita zai iya faxawa ciki, ke nan kamar irin su shi kansa habaici da hikimar ita kanta da sauransu. To ke nan a wannan ma'anar,

karin magana ta qunshi shi kansa habaicin kamar yadda yake sashi ne na hikima, kasancewa bayanin ma'anar na cewa karin magana zance ne mai qunshe da hikima, wato da shi da hikima ana iya gwama su. Kamar yadda a wasu harsuna kamar Larabci, karin magana da hikima kowanne na da ma'anarsa mai zaman kansa inda Al-Askandariyyu da sauransu (1980) suka nuna karin magana "zance ne taqaitacce wanda ake siffanta hali na biyu da na farko da shi". Wato wai abu ne wanda ya riga ya faru har an buga misali da shi ta hanyar karin magana sai kuma wani abu irinsa sak ya sake faruwa sai a xauko wancan hali na biyu a yi amfani da shi kamar dai na farkon don tabbatar da kwatanci ko daidaito a tsakanin halayen guda biyu. Misali Hausawa sukan ce "gaba ta kai ni, gobarar Titi". Wannan karin magana ce wadda take da tarihi. An ce abin da ya faru shi ne, Titi wata mace ce wadda take zaune a Jos. Wata rana abin Allah sai musibar gobara ta same ta. Titi ta yi hasara mai ximbin yawa inda ta girgiza ta qwarai. Amma kasancewar Titi mace ce mai mutune da yawa da abokan arziqi, sai suka tattara mata gudummawa mai yawa. Abin da ta samu har ya wuce abin da ta yi hasararsa. Sai mutane suka ga ita wannan gobara gaba ta ci da Titi ba baya ba. Shi ya sa ma duk wani wanda ya yi hasara ya samu abin da ya fi wanda ya yi hasara, yakan ce wa kansa "Gaba ta kai ni, gobarar Titi".

Kamar Hausawa su ma Larabawa suna da wannan karin maganar. Misali, wasu unguwanni na Larabawa sun yi hatsaniya a tsakaninsu, har 'yan wata unguwar suka kashe mutum xaya na xaya unguwar. A lokacin da ake ta

cece-kuce game da maganar sulhu a kan ’yan unguwar mamacin su karvi diyya. Sai wata baiwa wadda ake kira Juhaiza ta zo ba zato ba tsammani take faxin cewa ai ma wani daga cikin iyalan mamacin ko ’yan’uwansa ya ga wanda ya yi kisan har ma ya kashe shi. To sai masu sulhu suka ce Juhaiza ta yanke zancen duk wani mai zance. A nan Larabawa sukan ce (قطعت جُحيظ قول كل خطيبٍا) “*Qaxa’at Juhaiza qaula kulli khaxibin*”. Tun daga nan ake buga wannan misali ga duk wanda ya yanke wa mutane wata taqaddama da suke yi babu zato babu tsammani.

Kamar yadda ita hikima idan muka koma farkon zancenmu za mu ga yawanci zance ne wanda yake nuni zuwa ga aikata alheri ko kuma barin aikata sharri. A wasu lokutan za a ji Hausawa suna cewa “masu hikima sun ce”. Misali, masu hikima sun ce “in ka ga gemun xan’uwanka ya kama da wuta to shafa wa naka ruwa”, ko kuma “Gani ga wane ya ishi wane tsoron Allah”.

Savanin Zarruq da abokan talifinsa shi Umar (1986:11) cewa ya yi “karin magana na nufin wata ’yar gajeriyar jimla da mai magana kan faxa ta hanyar hikima amma kuma ta qunshi ma’ana mai yawa idan an tashi yin sharhinta”. Ita kuma mai bincike take ganin karin magana zai iya qunsar hikima da habaici da gargaxi da tsokanar faxa da hassada da dai sauransu. kamar yadda wannan bincike ya nuna lallai karin magana da habaici suna da alaqa suna kuma da ’yan bambance-bambance da ba su kai alaqarsu yawa ba.

Ke nan “habaici wani nau’i ne na zancen hikima da ake amfani da shi a yi da mutum a fakaice, yawanci habaici yakan qunshi kwatanta wasu abubuwa ne da nufin nuna gazawa, ko raini, ko mayar da martani ga wanda aka yi wa shi” (Umar, 1980:24).

Ke nan a nan ya fito qarara cewa shi habaici ko dai abokin gwami ne na karin magana ko kuma sashe ne na karin magana ko kuma ma shi kansa habaicin karin magana ne.

Kishiya kan ce a yayin da fitinar wani/wata ta gallabe ta ta so ta gaza ko kuma don nuna wa mai yin aikin tsananin munin aikinsa “ya na iya da abin da ya gagari wuta in ji kishiyar qonanniya”. Shin mene ne bambanci tsakanin wannan da misalin (Zarruq, 1986:45) “kowanne gauta ja ne sai in ba a sa shi a rana ba”, kuma wannan ana yi ne da wani ko wata waxanda ake son a fito da munanan xabi’unsu qarara ko nuna vacin aikinsu. A inda karin magana ya sami daidaito da habaici a nan wajen kushe hali. Hasali ma a wajen wasu dukkan waxannan misalai abu xaya ne a inda wasu kan kira shi karin magana wasu su kira shi habaici.

Duk da a wasu halayen kowanne kan ja matsayinsa a inda babu yadda za a yi a kira karin magana habaici, misali “Taka faifai rage zango ne ga mai hawa sama”, da kuma “in ka je gari ka ga kowa da wutsiya nemi kara ka laqa”. Waxannan karin magana babu yadda za ka yi ka kira su habaici domin kuwa ba su yi nuni da yi da mutum a voyen da Magaji (1980) yake cewa

“habaici shi ne yi da mutum a voye. Akan faxi wasu kamannu ko hali na mutum yadda daga ji ya san da shi ake yi”.

Amma a qarshe bincike ya gano cewa duk habaici karin magana ne, amma ba duk karin magana ne yake amsa sunan habaici ba. Habaici sashi ne na karin magana kuma da karin magana da shi kansa habaicin suna da alaqa da hikima kamar yadda kuma aka gane cewa duk hali wanda ake yin karin magana a kansa ko habaici yana faruwa ne a lokacin jefa masa maganar, to amma ita kalmar da aka jefar ba a nan take aka qirqire ta ba, hasali ma yawanci wanda ya qirqira ba a san shi ba.

3.3.1:2 Habaici a Take

Zarruq, da Wasu (1986:52) sun bada ma’anar take kamar haka:- Take xan’uwan kirari ne. Shi ma ana yabon mutum ne amma ba da lafazin baki ba sai dai ta hanyar kixa. Duk da haka wannan bai hana ka ji ana amfani da kalmomi wajen fassara abin da kixan take ke cewa ba. Sun qara da cewa wani bambanci tsakanin Take da kirari shi ne da wuya mutum ya yi wa kansa take kamar yadda zai iya yi wa kansa kirari. Muhimmin abu dai game da take shi ne, a san cewa ko da ana amfani da magana to kixan dai shi ne take.

Bincike ya gano take yana iya zama habaici a tsakanin al’umma maza ko mata, domin za a ji shi ainihin wani taken ma wani ake yi wa habaici,

musamman a dandali inda ‘yan mata da samari suke taruwa suna yin wasanni. Misali taken wata budurwa shi ne:

“Allurar cikin ruwa, mai rabo ka xauka”

Idan budurwa tana da masoya da yawa wanda ta fi so na iya sawa a kaxa mata take domin ya ba wa sauran samarinta haushi, saboda ganin duk da budurwar tana da masoya da yawa amma yana ganin a cikinsu ta fi son sa. Sannan kuma kaxa taken na iya zama yi wa wani daga cikin samarin nata habaici.

3.3.1:3 Habaici a Kirari

Kirari in ji, Zarruq da Wasu (1986:50) shi ne idan mutum yana wasa kansa ko yana wasa wani cikin daddaxan lafazi sai a ce yana kirari. Shi kirari haka yake, waqa-waqa, magana-magana, shi dai ba waqa ba saboda ba a rangwaxar murya, shi kuma ba magana kara-zube ba, saboda kana iya jin wani ko wata a cikinsa. Duk da haka akan sami kirari ya fito a cikin waqa.

Hausawa na yi wa abubuwa da dama kirari kamar Bil-Adama da muhalli da dabbobi da sana’o’i da abinci da sauransu.

Mai bincike ta gano shi kansa kirari na da alaqa da habaici, misali idan muka xauki kirarin muhalli, akwai kirarin garin Kano:

Kanon Dabo tumbin giwa,
Gari ba Kano ba jejin Allah,
Yaro ko da me ka zo an fi ka.
(Junaidu da ‘Yar’aduwa, 2007:90)

Bakano na iya amfani da jimla ta biyu a cikin jerin kirarin ya ce “Gari ba Kano ba jejin Allah”.

Wato ga mutumin da ba Bakano ba musamman in ya kai ziyara wani garin da ba Kanon ba don ya yi wa ‘yan garin habaici zai iya fadar haka.

Haka kuma akwai kirarin dabbobi, misali Giwa sai a ce:

Giwa bukkar daji,

Giwa kin wuce tarko,

Giwa cimar ki itace.

(Junaidu da ‘Yar’aduwa, 2007:90)

Habaici na da kyakkyawar alaqa da kirari domin za a iya danganta wannan kirari da wani basarake mai alfarma ga abokan gabarsa ko mahassadansa waxanda suke haqon sa, kuma a gaban su don a nuna ya fi qarfinsu.

3.3.1.4 Habaici a Zambo

Zarruq, da Wasu (1986:49) sun bada ma’anar zambo kamar haka, “zambo xan’uwan habaici ne, sai dai shi zambo ya fi habaici tsanani. Galibi idan an yi zambo wanda aka yi wa ya san da shi ake har mutane ma sukan san da shi ake. Muhimmin bambanci tsakanin zambo da habaici shi ne, zambo sai a waqa ake yinsa, ya kuma fi sauqin samuwa a waqoqin baka, musamman irin na fada. Akan yi wa mutum zambo ne domin a tozarta shi a idanun jama’a. Akan xauki hali ko siffa ta mutum a yi masa zambo da shi.

Habaici wani irin nau’in zambo ne, ya fi zuwa a kaikaice, watau a lulluve, domin a yayin habaici ba akan bayyana wata fitacciyar siffar mutum

ko wani halinsa na yau da kullum ba, sai dai akan yawaita amfani da kalmomi kamar su wane ko mutum ko waxannan ko waxanga ko waxancan ko wasu ko wata da makamantansu. Akan yi amfani da waxannan kamomi a kaikaice ba tare da sun danganci kowa ba, amma kuma za su iya shafar kowa xin domin shi habaici riga ce ake xinkawa duk wanda ta yi wa daidai ya xauka ya saka.

Sun qara da cewa zambo da habaici ba wai sun tsaya ga waxanda ke gabar sana'a ko hassada ga sarki ba, ana samun su tsakanin mawaqa ko kuma a cikin waqoqi, musamman na baka. Mawaqa na yi wa junansu xayan waxannan (zambo ko habaici) wurin gasar samun ubangida da makamantansu.

Akwai habaice-habaice da mawaqa maza sukan yi a cikin waqoqinsu. Amma mafi yawan jama'a sukan xauki irin waxannan maganganu na habaicin mawaqa a matsayin zambo. Zambo kishiyar yabo ne don kuwa ana faxin wasu miyagun abubuwa ne ga mutum. Ana iya ambaton halayen mutum masu kyau ko marasa kyau ko kuma a qirqiri wasu halaye da ba na mutum ba a sa masa don kawai a vata masa rai ko kuma suna.

Idan muka yi la'akari da abin da Xangambo, (1984:42) ya faxa "habaici yi ne da mutum da magana a voye". Za mu ga cewa zambo habaici ne a vangaren maza domin mawaqa kan yi wa mutum zambo tare da ambatar sunansa ko kuma su qi ambatar sunansa yadda ba za a gane da shi ake ba cikin hanzari, kuma rashin ambatar sunan nasa ya sa ya zama habaici.

Maroqa da mawaqan Hausa kan yi wa junansu habaici ko zambo, misali akwai wata waqa inda Alhaji Xanqwairo yake cewa:

Ga makaxi ya qulla waqa tai,

Sai a amsa mashi ba a qara mai,

In niq qulla waqa a qara min,

Mu huxu duk azanci gare mu,

(Safara'u, 1994:31)

Idan muka duba wannan waqa ta Xankwairo za mu ga habaici ne, kuma bai kira sunan wanda yake da shi ba sai dai ana zaton da Shata yake domin shi 'yan amshinsa suna maimaita abin da shi Shatan ya faxa ne, su kuwa 'yan amshin Xanqwairo suna qari a kan abin da ya faxa.

Akwai wata waqa ma da Ahmadu Doka ya yi ake zaton shi ma yana yi wa Shata habaici ne domin Shata ya mai da martani da ya zo daidai da waqar wadda ake zaton da shi Ahmad Dokan yake. Ga abin da Ahmadu Doka ya ce:

Wasu mawaqa na ta zage-zage,
Mu wasanmu babu zage-zage,
Kowacce waqa mutum yake yi,
Kukuma ba qanqanin kixa ne ba.

(Safara'u, 1994:32)

Mawaqa da dama kan yi zage-zage a cikin waqoqinsu wanda Shata yana xaya daga ciki, shi ya sanya ake zaton da shi yake.

Ga kuma abin da Shatan ya ce:

Wata rana a Kano birnin Dabo,
A zamanin Sunusin Mamman,
Yo had da Habu xan Abdu,
Da Sunusi ya tara mawaqan birni.
Ya kau tara maroqan qauye,
A zamanin nan,
Ana bukin ‘yan sarki,
Duk nan muka hallara qofar fada,
Ranar da na miqa na kama kirari,
Ina Alhaji ya gode wa Allah,
Mun gode wa Rasulullahi,
Lokacin da nah hana Hamisu,
Makaxin Caji Na hana Davalo ya daina,

Alo-alo mai ganga ya gode,
Yaran mai ganga sun gode.

Na qyale banjo da kukuma,
Wargin yara ne.

(Sanyinna, 2003:160).

Duk da Shata bai kira sunan Doka a waqarsa ba ya ce *banjo da kukuma* wanda kowa ya san shi Dokan da kukuma yake kixa.

Kusan kowanne mawaqin baka yana da na sa habaici, ga abin da Narambaxa yake cewa a waqarsa:

Maxi bai kai ya zuma ba,
Kowal lasa shi ka hwaxi,
Kwandon wake bai kai ga damin gero ba,

Xan akuya ko ya yi qahonni,
Ka san bai yi kamar rago ba.

(Waya, 1990:27)

A wannan waqa Narambaxa bai tantance wanda yake wa habaici ba amma tabbas da mutane biyu yake inda ya nuna xaya ya fi xaya.

Bincike ya gano zambo shi ne habaicin da mafiya maza suke amfani da shi koma bindiga ce da duk ilahirin mawaqa ke amfani da ita, yana da matuqar muhimmanci a wurinsu domin suna firgitar da jama'a da shi.

ii) Rubutaccen Zube:

Rubutaccen zube ya samu ne ga Bahaushe da farko bayan zuwan Musulunci na biyu kuma bayan zuwan Turawa, domin ga alama kafin zuwan Musulunci babu wani rubutu balle ma a ce akwai littattafai irin na qagaggun labarai ko akwai ma dai Hausawa ba su riske su ba.

Bayan zuwan Turawa an sami rubutun zube tun daga kan zuwan Turawan farko da kuma Turawan mulki. Daga cikin irin waxannan rubuce-rubuce akwai irin su *Shaihu Umar* da *Ruwan Bagaja* da su *Jiki Magayi* da sauransu.

Ga misalin habaici a cikin zube.

Akwai littafin *Jiki Magayi*, inda Zainabu take mayar wa da Abubakar martani da magana ta sigar habaici, ga abin da ta ce "ai ka sani budurwa haja ce, kowa ya gani yana so, kowa kuwa da irin tayinsa, amma mai saye xaya ne". (Umar, 1995:09).

Akwai kuma inda kishiyoyinta (Zainabu) suka riqa yi mata habaice-habaice da cewa “irin aure-auren ke na, har an je an auro wadda za ta haifi mugun xa! Da haihuwar varawo gwamma vari”. (Umar, 1995:41).

3.3.2 Habaici A Waqa

Xangambo, (2007:6) ya bada ma’anar waqa kamar haka “waqa saqo ce da aka gina shi kan tsararriyar qa’ida ta baiti, xango, rerawa, kari (bahari), amsa-amo (qafiya) da sauran qa’idojin da suka shafi daidaita kalmomi, zavensu da amfani da su cikin sigogin da ba lallai ne haka suke a maganar baka ba.

Waqa iri biyu ce, amma wajen bada ma’anar kowace sai an yi la’akari da kalmomin da suka jivinci kowace kafin ma’anarta ta fito. (Xiso, 2009:2).

i) Waqar Baka
ii) Rubutacciyar Waqa

i) Waqar Baka: Ita ce irin waqar da ake qirqirarta da ka a aiwatar da ita da baka (watau a gudanar da ita da baka ba a rubuce ba), sannan kuma a adana ta da ka. Irin wannan waqar akan yi ta ne tare da kixa na ganguna iri-iri ko qwarya ko busa ko goga wani abu kamar irin su yizga ko tsirkiya da abubuwa irin su goge ko kuma gurmi, garaya da sauransu.

Waqa na da kyakkyawar alaqa da habaici, domin akwai habaici na cikin waqa, ko dai mawaqa masu zaman kansu ko kuma waqe-waqen da ake

yi a tsakanin mata a vangaren makaxa na gargajiya. Za a samu kowane mawaqi yana da nasa tilon habaicin. Misali Musa Xankwairo a wata waqa da ya yi wa Sarkin Daura, Alhaji Muhammad Bashar, cewa ya yi:

"Wane ga ka xan Musulmi,
amma sabga kakai ta arna"

Wannan waqa na nuni ne a kan wani mara hali mai kyau, amma kuma shi Musa Xankwairo bai ambaci sunansa ba wanda shi wannan mutum Musulmi ne amma kuma ayyukansa sun sava da na Musulmi.

Haka kuma wata waqa ta Salihu Jankixi cewa ya yi da nufin nasa habaicin:

"Ga wani ya yi vatan vakatantan,
Ba ya ga tsuntsu ba ya ga tarko,
qaqa yay yi da xaukar bashi,
A'a yay yi da xaukar bashi.
(Waya, 1990:25)

A nan ma Jankixi habaici yake yi wa wani mutum wanda yake xan Sarki ne ya nemi sarauta ya kashe kuxi a neman wannan sarauta har ma ya haxa da cin bashi amma bai sami biyan buqata ba, a qarshe ya yi biyu babu, babu kuxi, babu sarauta, ga kuma bashi da ya tara wa kansa.

Haka ma Alhaji Mamman Shata a cikin wata waqa tasa mai suna don Sallah da Salatil-Fati inda yake cewa:

Don na ce mata ku yi aure,
Kaxo ya so ya wulaqanta ni.

(Sanyinna, 2003:2).

Baya ga habaice-habaice a waqoqin makaxa da mawallafa akwai ire-iren habaici a cikin waqoqin mata na tafiyar da harkokinsu na yau da kullum, kamar lokacin daka ko niqa da dai sauran ayyuka da makamantansu.

Misali akwai wata waqar da take cewa:

"Ana lugude ana mama,
Cikin shigafa cikin soro,
Mama ba habaici ce ba,
Salon daka a haka nan,
Ga macen da ba a so ta haihu,
Ta haifi qwandamin xa namiji,
Shugaban daka shi ka daka,
'yan tayyo kissa sukai,
Sukus-sukus sai su aje,
Gidan marafa ko ka ji daka,
Turmami na izon wuta,
Angulu ka kirva dawo".

(Binta, 1998:134)

Akwai kuma inda Barmani Coge ke nata habaicin cikin waqa ga abin da ta ce:

"Waxansu na ba mu kuxi,
Waxansu na zagin mu,
Ina ruwan wani da wani,
In ba rashin kunya ba,
Ana zama da varawo,
Bare maroqin baki".

(Safara'u, 1994:36)

Daga jin wannan na waqa an san mawaqiyar tana maida martani ne ta sigar habaici ga wasu da suke kushe ga wannan sana'a tata ta waqa.

- Akwai kuma wani misalin a waqar Hauwa Mai Amada a waqarta ta Kishiya, ga abin da ta ce:

"Malam xauko kuxinka mu je gabas,
Malam xauko allonka mu je gabas,
Sai ta ce ai ko Ikko ne zan bi ku,
Ashe karyar na nan maqe,
Ai kin ji ko 'yar Ali,
Wani mutum ba shi da zuciya,
Gara kare ma da shi".

(Safara'u, 1994:36)

Daga jin wannan waqa an san ana yi wa kishiya habaici ne inda aka danganta ta da karya saboda naci.

ii) Rubutacciyar Waqa: Wannan ita ce nau'in waqar da ko da yake dai a ka ake fara qirqirarta, amma ana rubuta ta ne a takarda ta hanyar zaven kalmomin da suka dace da auna su da kuma saka su gurbin da ya dace da baiti da amsa-amo ko qafiya da kuma uwa-uba abin da ake kira kari ko bahari.

3.3.3 Habaici a Wasan Kwaikwayo

Xangambo, (1980:12) ya ce ma'anar wasa kwaikwayo kamar yadda sunan ya nuna, wasa ne da ake gina shi kan kwaikwayon wani labari, ko

wata matsala ta rayuwa da ake son nunawa ga jama'a. Akan aiwatar da labarin matsalar da sauransu cikin siffar "yaqini" wato zahiri.

Akwai kyakkyawar alaqa tsakanin habaici da wasan kwaikwayo domin akan aiwatar da habaici a wasance, ma'ana a cikin rubutaccen wasan kwaikwayo na Hausa, ga misali daga littafin *Jatau na Kyallu*, ga abin da uwar gidan Malam Jatau ta ce: "... ai kowa ya sayi rariya wallahi ya san za ta zubad da ruwa". Manufarta a nan ita ce duk wanda ya auri karuwa ya san za ta vata gidansa ne.

3.4 Habaici a Zantuttukan Yau da Kullum

Habaici abu ne da ke da matuqar muhimmanci ga al'umma, musamman ta hanyar gabatar da zantuttukansu na yau da kullum.

Habaici cikin zantuttuka na yau da kullum habaici ne da ake iya gina shi kan kowane irin abu da ya shafi kama ko siffa ko hali ko xabi'a ta mutumin da ake yi wa, kai wani lokaci ma har da yanayin da kan faru tsakanin al'umma.

Irin wannan habaici za a iya kasa shi gida biyu:

a) Kamar yadda bayani ya gabata a baya cewa habaici xan'uwa ne ko kuma sashe ne na karin magana shi ya sa Hausawa kan yi amfani da karin magana waxanda suke shiryayyu, tsararru waxanda da ma can sun tsara su, kuma a haka ake faxarsu wajen aiwatar da habaici. Misali:

- Akuya ba ta gasa da kura
- Kaza mai ‘ya’ya ita ke gudun shirwa
- Kowa ya ci tuwo da ni miya ya sha.
- Ku taya ni figa uwar miji ta zama kaza.

Za mu ga duk irin waxannan misalai na cikin wannan kashi da ma can tsararru ne, akwai su ana amfani da su, kawai jira ake yi abu mai alaqa da su ya faru a jefa wa mutum su. Wannan nau’i na habaici shi ne yake fitowa a sigar karin magana.

b) Akwai kuma wanda shi mai yin habaicin zai qirqira da kansa amma kuma da ya yi za a gane habaici yake yi. Ma’ana shi ba an tsara shi ba ne, kawai yana zuwa ne cikin maganar yau da kullum, don shi ba ajiyayye ba ne kawai a lokacin da abu ya faru ake jefa shi. Misali:

Wasu mata guda biyu sun yi faxa to bayan an sasanta su kuma komai ya yi daidai, sai wata akuya ta zo wucewa kusa da xaya daga cikin matan. Sai cewa ta yi wannan qeqasasshiyar akuya ramammiya ta yi kama da mutane.

To a nan za a gani nan take ta qirqiro habaici wanda ya yi dai dai da halin da ake ciki ba tare da tsara shi kafin lokacin faruwar abin ba.

Kamar kuma yadda ake ba da labarin wata mata da mijinta sun yi rigima inda matar ta zargi mijin nata da rashin yin wanka. Saboda

wannan zargin sai ya sake ta ya kuma qara da ce mata, to sai ki tafi ki auri agwagwa, ni kuma zan auri akuya.

3.5 Kammalawa

Wannan babi da ya gabata ya yi nazari a kan habaici tare da bin dangantakarsa da sauran zantuttukan hikima na Hausa kasancewar da yawa daga cikinsu gurabensa ne.

Baya ga duba da babin ya yi a kan dangantakar habaici da karin magana da take da kirari da zambo, babin bai yi qasa a gwiwa ba sai da ya duba yadda habaici ke wakana a zantuttukan yau da kullum.

BABI NA HUXU: JIGOGI DA AMFANIN HABAICI

4.0 Gabatarwa

Jigo kalma ce da masana adabin Hausa suke yin amfani da ita da nufin maqasudi ko manufa ko kuma saqo da mai rubutu ko bincike da sauransu ke son bayyana wa jama'a.

Wannan babi xauke yake da bayani kan jigogin habaici tare da matsayinsa ga al'ummar Hausawa ta vangaren mata da kuma maza.

Babin bai tsaya kan bayyana yadda mata Hausawa ke amfani da habaici don kushe da faxakarwa ba kawai, sai da ya yi tsokaci kan amfanin habaici wajen faxakarwa ta vangaren addini.

4.1 Matsayin Habaici ga Al'ummar Hausawa

Hausawa al'umma ce da ke zaune a Arewacin Nijeriya da wani yanki na Nijer da Chadi, waxannan jama'a sun kasance mutane ne masu al'adu da xabi'unsu na asali wanda ya sa cakuxa da sauran al'ummomi kamar Labarawa da Turawa ya yi tasiri game da al'adun nasu.

A Bahaushiyar al'ada namiji ke jagorancin gida, aikin mace kuma ya haxa da:

a) rainon yara

b) dafa abinci da kuma

c) kula da gida.

A zamanin da mace ba ta da daraja sosai a gurin Bahaushe domin sai yadda maigida ya yi da ita, ba za ta je makaranta ko aiki ba, bare uwauba ta yi siyasa. Bayan zuwan addinin Musulunci da Turawa sai wannan al'amari ya sauya. (Azima, 2007).

Bahaushe kafin zuwan Musulunci yana da damar auren mata ko guda nawa ya ga zai iya ba tare da qayyadewa ba. Wannan ya dogara ne da halin da yake da shi. A wurin su auren mata da yawa wata hanya ce da mutum zai qara tattalin arziqinsa. Domin babbar sana'ar Hausawa a wannan lokaci ita ce noma, idan kuma an tashi noman tare ake yi da mata. Wato wanda yake da mata da yawa gonakin da zai noma suna da yawa ke nan, don haka amfanin gonarsa ma zai yi yawa.

Bayan zuwan Musulunci sai ya zamana Bahaushe ba shi da ikon ya auri mace fiye da huxu, kai in har ba zai yi adalci ba, bai kamata ya auri fiye da xaya ba ma.

Matan Hausawa sun saba zama da kishiya, don haka idan namiji ya auri mace fiye da xaya sai su yi zamansu tare a gidan mijin. To da yake yau da gobe sai Allah, wannan zama da suke tare kan sa a sami rashin jituwa a tsakaninsu, saboda kishi wanda ke haifar da yin habaici a tsakaninsu domin cimma wani buri na rayuwarsu.

Bincike ya nuna asalin kalmar habaici ba za a iya danganta ta da wani harshe ko wata qabila ba, ban da Hausa. Ma'ana an sami kalmar habaici daga harshen Hausa ba tare da an aro ta daga wata qabila ko wani harshe ba.

Wannan ya tabbatar da Bahaushiyar kalma ce wadda ba za a iya cewa ga lokacin da aka fara amfani da ita ba. Habaici yana daga cikin maganganun hikima da nuna gwaninta da naqaltar harshe da Hausawa suka gada iyaye da kakanni.

Hausawa sun taso suna shirya habaicinsu da ka ne a cikin maganganunsu na yau da kullum ko a cikin waqoqi, sannan su adana abinsu da ka. Habaici yakan sami ci gaba dangane da juyawar lokaci ko zamani.

Bincike ya nuna a harshen Hausa ita kalmar habaici an gina ta ne daga abin da aka yi shi bayan wani abu ya faru. Ka ga a nan "xan baicinka" na nufin xan bayanka ke nan. Haka kuma idan an ce "ni da kai muka yi maganar baicin ya san an je an yi alqawari da shi a kan abubuwan. Wannan kalmar *baicin* tana nufin bayan wani abu ya faru ke nan.

Haqiqa yanzu ba za a iya cewa ga zamanin da al'ummar Hausawa suka fara yin amfani da habaici a cikin maganganunsu ko rayuwar su ba. To amma an samu Hausawa suna yin habaicin tun daxewa, haka kowa ya taso ya tarar Hausawa suna shiryawa da ka kuma suna faxar abin su da baki a cikin waqoqi ko a cikin maganganunsu. Haka kuma ma'anar habaici ba ta canzawa, sai dai ana samun sababbin habaici dangane da ci gaban al'ummar wajen qere-qeren da harshen ke yi na sarrafa harshen ko kuma saboda yanayin wannan zamanin da ake ciki.

Habaici abu ne mai matsayi ga al'ummar Hausawa kamar yadda sauran kashe-kashen adabin baka ke da matsayi, don shi ma ya qunshi hikimomi na sadarwa tsakanin al'ummar.

Habaici abu ne wanda al'ummar Hausawa suke amfani da shi yau da kullum wajen zantuttukansu. Saboda haka ashe habaici yana da matuqar matsayi ko a ce muhimmanci ga al'ummar Hausawa kamar yadda sauran adabin baka suke, wato su waqa da karin magana da tatsuniya, waxanda kusan kullum sai an yi amfani da su.

Saboda irin matsayin da habaici yake da shi ga al'ummar Hausawa ya sa ya zama muhimmi a gurinsu ta vangare daban-daban.

4.1.1 Habaici Tsakanin Maza

Habaici ya fi yawa a inda kishi ko qyashi yake. Galibi mutane suna xauka habaici salon mata ne saboda a tsakanin mata kishi da qyashi suka fi yawa.

Amma abin ba haka yake ba domin ana samun habaici a mata, ana kuma samun sa a maza. Dangane da nazarin habaici tsakanin maza abu ne da ya kasance su ma suna amfani da shi, musamman idan suna gaba ta sana'a ko neman aure ko sarauta ko kuma wani abu na ci gaba, sukan yi wa juna habaici.

4.1.2 Habaici Tsakanin Mata

Habaici abu ne mai matsayi da yake da cikakken tasiri ga rayuwar matan Hausawa.

Idan aka ce tasiri ana nufin cuxanyar wani abu da zai shafi wani dangane da xabi'arsa ko halayensa ko ayyukansa kuma ya sami rinjaye a kansa. Wato ke nan tasirin habaici ga rayuwar mata yana nuni ne kan yadda habaicin ya shiga cikin zuciyarsu ko jikinsu ta hanyar cuxanya, kuma da matuqar muhimmanci ga rayuwarsa.

Mata suna amfani da habaici wajen furta ko fitar da abin da zuciyarsu ta qunsa na takaici ko suke so su qunsa wa wani, domin habaici ya qunshi hikikomi na sadarwa tsakanin al'umma don haka suke amfani da shi don isar da duk wani saqo da ke zuciyarsu.

Habaici abu ne da mata suke amfani da shi yau da kullum wajen zantuttukansu. A wasu lokuttan ma sukan yi habaici ba tare da sanin sun yi ba. Saboda haka ashe habaici yana da matuqar matsayi ko a ce muhimmin abu ne ga rayuwar mata.

Matsayin habaici ga rayuwar mata abin yana da yawa da kuma faxi. Domin abu ne da ya shafi wani vangare na al'adunsu, wanda rayuwarsu kuma tana tafiya ne tare da al'adunsu. Habaici qunshe yake da hikimomi wajen yin sa. Daga cikin su akwai sarrafa harshe da kamantawa da kushewa da kuma raya al'ada da inganta su. Haka kuma amfani da habaici da mata suke yi a cikin harshensu yana daxa musu muhimmanci da matsayi, saboda

harshe yana samun martaba dangane da hikimomin da ke tare da shi, kamar sarrafa harshe, nuna gwaninta da fasaha tare da qarfafa tunanin mai amfani da shi. Haka kuma yana daga matsayin habaici ga mata cimma burin abin da ke zuciyarsu da kuma sanya su tunani a kan abin da za su yi, ko su faxa.

Haka kuma yana daga cikin matsayin habaici ga rayuwar tasu, in sun yi shi za su sami farin ciki a ransu da jin daxi saboda sun huce takaicinsu game da abin da ya dame su. Haka kuma sun xauke shi hanya ce da za su yi wa mutum wani abu wanda nan da nan za su rama cuta ko wani abin vacin rai da aka yi musu.

Baya ga taimaka wa mata da habaici yake yi wajen fitar da abin da yake zuciyarsu ko su qunsa wa wani, yana kuma matuqar taimaka musu wajen taqaita magana domin isar da kowane irin saqo. Kasancewar mata jinsi ne masu rauni akasari suna son abu mai sauqi ne ba mai wahala ba, shi kuma zancen habaici taqaitacce ne don kuwa mafi yawan habaici ba su fi jimla xai-xai ba, mai yawan ne ma zai kai jimla uku. To wannan hikima ce babba da mata suke da ita don taqaita magana. Za a ga sun yi magana kaxan amma in an zo bayyana ta sai an kusan cika shafi fiye da xaya. Alal misali “Hantsi leqa gidan kowa”.

Idan muka xauki wannan habaici za mu ga kalmomi ne guda huxu rak, amma idan aka tashi bayyana su za a ga ma’anarsu tana da faxi. Za a iya jefa wannan habaici ga matar da take mugulmaciya ce ko take yawan shiga

gidaje yawon gulma da haxa faxa. To ‘yan’uwanta mata suna iya jefa mata wannan habaici da zarar sun gan ta.

Mata sukan yi amfani da habaici a rayuwarsu yayin biki ko suna ko wani sha’ani don yin gargaxi ga ‘yan’uwansu mata game da wani abu na rayuwa. Wani lokaci akan sami wasu su riqa aikata wani abu na ba daidai ba, ana kuma tsoron a tare su gaba da gaba a gaya musu. Saboda girmansu don kada ransu ya vaci. To, a nan sai a yi amfani da habaici don a gargaxe su ko a ba su shawara. Ta hanyar habaici waxannan mata za su iya gane ana yi musu hannunka mai sanda ne in an ci sa’a sai su xauki wannan shawara.

Baya ga abubuwan da aka faxa a baya ana iya cewa matsayin habaici ga rayuwar mata abu ne halittacce, wanda yake a cikin jininsu. Kowane matsayi na rayuwa suke suna iya amfani da habaici don kushe abokan hamayyarsu ko cimma wata manufa tasu.

Saboda zamewa jiki da habaici ya yi ga mata ba wai suna saka shi a cikin magana kawai ba ne, sukan saka shi a cikin waqa su riqa rerawa ko su aiwatar da shi yayin da suke gabatar da wasu ayyukansu na gida.

4.2 Jigogin Habaici

A xabi’ance kusan kowace wallafa ko qirqira na da saqon da mai yi ke son isarwa, haka ma yake ga habaici, domin akwai saqonni da ake da su don isar wa ko dai masu kyau ne ko kuma marasa kyau. Daga ciki akwai habaici don kushe da kuma don faxakarwa da habaici don wa’azi.

4.2.1 Habaici don Kushe

A duk lokacin da aka ambaci kushe ana magana ne a kan gazawa ko kasawa ko kuma rashin cika na wani abu wajen amsa sunansa.

Kushe wani yanayi ne da kan sa yin habaici kasancewar ba a rasa ‘yan kace-nace a tsakanin al’umma da kuma faxace-faxace.

Mata ko ma maza kan kushe junansu ta wani vangare da suka gaza ta hanyar amfani da habaici, walau a zance na yau da kullum ko kuma a waqe.

Daga cikin abubuwan da ke haifar da kushen sun haxa da:

i) Nuna muni

ii) Nuna talauci

iii) Nuna tsawo da qiba da sirantaka da sauransu

iv) Nuna qazanta

v) Nuna wata naqasa

vi) Nuna son iyawa da makamantansu

Dangane da waxannan naqasu akan yi amfani da ire-iren habaici kamar haka:

- Sauna kamar a kife ta da kwando
- Kunkuru yana son dambe damtsensa ya gaza
- Haka tara, in ji kishiyar mai magexuwa
- Ala suturi buqui, in ji kishiyar mai doro, da makamantansu.

Haka kuma mata kan yi amfani da habaici don kushe wata halitta ta wata a waqe wajen gudanar da ayyukansu na gida. Ga misalin habaicin da wasu kishiyoyi su uku suka riqa yi wa amaryarsu ta hanyar lugude.

Ga mutum biyu a xaka idanunsu uku,
Su xauki xaya su raba,
Mu san zaman soyayya,
Ana daka tana xaka da miji,
Sannu mai miji.
(Rabi, 1998:43).

Da an ji wannan magana ka san habaici ne ake yi wa amaryar da take xaki ita da miji. Ita kuma amaryar tana jin wannan habaici sai ta gane da ita ake sai ta fito ta xauki tavarya ta fara mayar da martani kamar haka:-

“Sannu mai daka,
Sannu mai daka, Kwari

Ko da ban iya magana ba,
Ai nikan maida kari.

A zunkuxo maqoqo,
Makarin kururuwa.

Magexin magana,
Mele ka ci ka bari.

Ko amshi tavaryarku,
Baquwar za ta xaka.
(Rabi, 1998:44)

Habaicin da aka yi wa amaryar na nuna cewa ba ta fito an yi daka da ita ba, sannan kuma sun yi mata ba'a da cewa idonta xaya ne. Da jin wannan ita kuma sai ta fito ta mayar wa da kishiyoyin nata martani kasancewar su ma suna da abin faxa. A zunkuxo maqoqo na nufin xaya daga cikinsu tana da maqoqo, magexin magana kuma xaya na da magexuwa, sannan mele ka ci ka bari na nufin cikon ta ukun tana da mele. A nan amaryar ta maida martani akan abin da suka yi.

Habaici wani ginshiqi ne ga rayuwar mata domin suna iya amfani da shi kowane lokaci don cimma buri na rayuwarsu ko don nishaxi. Misali, wani lokaci mace za ta yi wanka da kwalliya a gidan mijinta ba tare da an mata komai ba ta saki habaici musamman in ta fi kishiyarta iya abinci ko kyau ko kuma iya kwalliya.

4.2.2 Habaici don Faxakarwa

Duk da cewar ana amfani da habaici don huce takaici ko tsokanar faxa ko muzgunawa ko ramuwar gayya ko kushe da makamantansu, amfanin nasa bai tsaya a nan ba don har akan yi amfani da shi don faxakarwa a kan abubuwan da suka shafi zamantakewa, wanda amfani da wannan habaici kan sa mutum ya gyara musamman kan abubuwan da suka shafi:

i) Tsafta

ii) Magana

iii) Girki

iv) Biyayya

v) Soyayya da makamantansu.

Ire-iren waxannan habaici sun haxa da:

- Wata ta dafa ta sayar wata ta dafa ta zubar
- Bin na gaba bin Allah
- So mai sonka, son maso wani cuta, da makamantansu.

4.2.3 Habaici don Wa'azi

A wannan bincike idan aka ce addini ana magana ne a kan addinin Musulunci duk kuwa da akan sami habaici a wasu addinan daban.

A halayyar zamantakewa ta xan Adam ana gudanar da habaici ne don kushe wani ko nuna gazawa ta wani ko wasu a kan wata halayyarsu ta yau da kullum.

Allah ya halicci xan Adam ne domin ya bauta masa, wanda savanin haka na iya jefa mutum cikin fushin mahalicci wanda shi aka fi sani da savo.

Baya ga nan Allah ya azurta xan Adam da baiwa ta fannoni daban-daban na rayuwa waxanda suka haxa da magana tare da nuna qwazo da qwarewa a vangaren harshe.

Wannan baiwa da Allah ya bai wa xan Adam ta vangaren magana ta sanya shi kushe wanda ko waxanda suka sava wa nufinsa. Baiwar ba ta tsaya a nan ba sai ta kai har xan Adam yana amfani da ita wajen wa'azi, wanda wannan kushe shi ake kira habaici a harshen Hausa.

Baya ga baqantawa da muzgunawa da mata kan yi wa abokiyar zama ko maqwabciya ta hanyar habaici, ci gaban ilimi da wayewar kai ta sa har sukan yi amfani da shi wajen gyara ko faxakarwa ta fuskar addini ko sha'anin rayuwa wanda bai tsaya ga su kaxai ba ma har sauran al'umma.

"Habaici a halayyar xan Adam abu ne halittacce da yake cikin jininsa wanda wannan ya sanya yake amfani da shi ta fuskoki daban-daban na rayuwarsa da suka haxa da vangaren addini". (Dunfuwa, 2005:25).

Kasancewar in an yi wa mutum habaici yana jin ciwo ya kuma yi qoqarin gyara abin da aka gargaxe shi ko faxakar da shi a kai ya sanya malaman addini da sauran jama'a amfani da habaici don wa'azantarwa ga jama'a ko faxakar da su a kan abubuwan da suka shafi rayuwar addini.

Da yawa daga cikin irin waxannan habaice-habaice kan amsa sunan habaici ne bayan nazarinsu a aikace, idan kuma an yi la'akari da bayanan mu kan dangantakar habaici da karin magana suna iya tsayawa a matsayinsu na karin magana. Haka kuma a wasu wuraren akwai misalai da suka shafi zantuttukan azanci na Bahaushe.

Akasarin waxannan habaice-habaice kan ko dai nusar ko faxakar ko wa'azantar dangane da abubuwan da suka shafi rayuwa ko kuma addini savanin na baya da kan muzguna ko baqantar.

Alal misali akwai habaici da yake cewa (Jan ido ba ya kawo kwarjini sai ikon Allah).

Idan aka dubi wannan habaici za a ga yana nuni ne ga jama'a a kan duk wani abu da mutum ya yi qoqarin yi wa kansa, kuma kowace irin hanya ya bi idan ba Allah ne ya ba shi wannan abu ba to ba zai same shi ba. Wannan zai sanya jama'a su yi haquri domin zafin nema ba ya kawo samu, wanda Ubangiji (SWT) ne ya umarce mu da yin haqurin. Hasali ma saboda darajar haquri Allah ya nuna mai yin sa yana tare da shi.

(Komai na duniya wuqar fawa ne, ya yanka guzuma ya yanka karsana).

Idan aka dubi wannan habaici za a ga yana nuni a kan ita rayuwar duniya ba a hannun mutum take ba a hannun Allah take, domin dukkan abin da ke cikin ta mai daxi ko mara daxi da arziqi ko talauci da ilimi ko jahilci da lafiya ko cuta suna iya samun kowa mai kuxi ko mara shi da talaka ko basarake, tunda Allah ne yake juya lamarin. Don haka gabatar da wannan habaici ga mutum na iya tunasar da shi cewa idan ya ga wani a cikin hali mai kyau ko mara kyau Allah ne, haka shi ma ko a wane irin hali ya tsinci kansa to Allah ne. Sannan zai daxa fauwala wa Allah idan wani abu ya same shi wanda shi ne yarda da qaddara, wato xaya ne daga cikin shika-shikan imani.

(Mutanen duniya su kai mutum inda Allah bai kai shi ba su wahalshe shi).

Idan aka dubi wannan habaici za a ga ana yin nasiha ne ga mutum a kan ya tsaya a inda Allah ya ajiye shi kada ya daka ta zugar mutane, ya yi amfani da hankalin da Allah ya ba shi wajen gudanar da harkokinsa na

rayuwa. Ma'ana idan ya daka ta mutane zai sha wahala, domin ba kowa ne Allah yake ransa ba, saboda haka wani yana iya saka shi ya yi wani abin da ba daidai ba a qarshe kuma ya sha wahala. Sannan kuma habaici yana daxa yin nuni da duk wani matsayi da aka ga mutum a kai Allah ne ya kai shi.

(Wanda bai gode wa Allah ba ya gode wa azabarsa).

Wannan habaici ne da yake nuni ga jama'a da su riqa yin godiya ga Allah kar su raina, baiwar da ya yi musu. Idan ma sun raina baiwar da Allah ya yi musu tana iya yankewa, idan kuma ta yanke ba su da yadda za su yi sai dai haqurin domin kuwa ba za su iya dawo da ita ba. To a nan za a ga da yin haqurin dole gara gode wa Allah domin za a sami lada, sannan a sami qarin wata baiwar. Dalili, Allah ne ya faxi cewa "in kuka gode Mini sai in qara muku" a cikin alqur'ani mai girma.

(Zakaran da Allah ya nufe shi da cara, ko ana muzuru ana shaho sai ya yi).

Wannan na nuni ne da daxa qarfafa ikon Allah. Mutum ya yi imani ya kuma tabbatar wa da kansa babu wani mai yi sai Allah domin duk qoqarin da mutum zai yi na wani abu ikon Allah ya sha gabansa. Idan Allah ya yi nufin xaukaka mutum ko kuma ya ba shi wani abu na alheri to idan da duk duniyar nan za ta haxu a kai ba a isa a hana shi samun wannan abu ba. Haka idan Allah ya qaddara mutum zai taka wani matsayi ko muqami na rayuwa to babu wanda ya isa ya hana shi. Har ila yau wannan habaici yana daxa

wa’azantar da mu cewa hassada ba ta da kyau wadda a addini tana cinye kyawawan ayyuka ne don haka barin ta shi ya fi alheri.

(Gobara daga kogi, magani nata Allah).

Wannan habaici nasiha ce ga jama’a kan duk wani abu da ya gagari xan Adam to akwai maganinsa a wurin Allah. Wannan na iya qara wa xan Adam qarfin imani a kan lamarin Allah cewa babu abin da zai gagare shi.

(In duniya ta shimfixa maka tabarma to zauna a gefe).

Wannan habaici yana nuni ne ga xan Adam ya guje wa duniya. Ma’ana ya yi takatsantsan da ire-iren ruxinta wanda yana iya halakar da shi, ya zo a banza, ya kuma koma a banza. Wannan ya zo daidai da faxar Manzon Allah (SAW) cewa: “Ka guji duniya, sai Allah ya so ka”. Sannan kuma yana daxa nuni ga cewa kada ka bari wani qyalqyali na duniya ya shagalar da kai a banza.

(In Allah ya so falke, sai kayansa ya tsinke a gindin kaba).

Wannan habaici na daxa jaddada qarfin ikon Allah da faxakar da jama’a cewa idan Allah ya nufi mutum da alheri yakan ba shi wata baiwa ta abubuwa masu kyau da za su zo daidai da yadda mutum yake so. Don haka, wannan habaici yana nuni da duk abin da aka gani na alheri game da wani to Allah ne yake yi kuma ya yi masa, ba mutum ba.

(Wanda Allah ya tarfawa garinsa nono ba zai sha da tsamiya ba).

Wannan habaici na yin nuni da a sani Allah ne yake da qarfin yin komai. Sannan idan ya rufa wa mutum asiri to ya rufa ke nan sai dai ya nemi wani abu daban a wurinsa.

(In Allah ya qi addu'ar biri, sai ya mutu a gonar arna).

Wannan habaici na nuni da abin dai da Allah ya so shi ake yi ba wai zavin mutum ba, sannan yadda ya so haka zai yi da kowa. Wannan na iya qara wa mutum imani da yin Allah shi ne yi ba yin mutum ba.

A qarshe binciken ya gano cewa lallai ana amfani da habaici don faxakarwa ta fuskar addini kamar yadda aka gani daga misalai da aka bayar. Sannan da yawan habaice-habaicen da ake da su na iya yin amfani wajen faxakarwa domin sukan dace da kowane irin yanayi.

4.3 Amfanin Habaici

Habaici abu ne da ke da matsayi da matuqar mihimmanci ga al'ummar Bahaushe dangane da irin rawar da yake takawa ta vangarori daban-daban. Daga ciki akwai:

4.3.1 Burgewar Harshe:

Habaici wata hanya ce da harshe ke nuna azurtarsa da havakarsa da cancantarsa ga rayuwar bahaushe. Ga shi dai habaici magana ce cikin Hausa wanda ake yi da harshen Hausa, amma saboda irin dabarun da ake yi wajen yin sa da kuma kasancewar sa ado ga harshe, ya sa da wuya wanda ba Bahaushe ba ya gane abin da ake nufi idan an yi masa,

kai wani lokaci har da Bahaushen ma kansa. Misali idan aka sami wanda ba ya jin Hausa aka ce masa

(Ature ba ya raba kare da kura).

Shi a iyakar sanin sa zai xauka ana magana ne a kan kare da kura, bai san cewa da mutum ake ba. Akan yi amfani da dabbobi ne don a sakaya domin ainihin maganar habaici tana da voyayyiyar manufa kamar inda Magaji, (1980) ya bayyana habaici da cewa magana ce mai voyayyiyar manufa. Wanda wannan ya sa habaici na burge al'ummar Hausawa.

Wani misali na burgewar harshe da habaici ke yi shi ne, an yi wasu kishiyoyi biyu, xaya 'yar liman ce, xayar kuwa sunan mahaifinta Baqo. Rannan suna zaune, sai 'yar tankiya ta shiga tsakanin su. Aka sulhunta su, suka haqura. Ana nan har an manta da maganar, rannan 'yar Baqo ta tayar da fitina a cikin habaici. Suna hira da Isha sai ta ta da kanta sama, ta dubi wata, ta ce "Kai yau wata yana qwalla haske", "qwalliman". Ko da 'yar liman ta gane manufa, ita ma sai ta dubi watan ta ce lallai ya qwalle duniya baqwalalacewa"

Babu shakka a wannan habaici an nuna gwanintar harshen Hausa, wanda in ba mutum ya cika Bahaushe ba, a Bahaushen ma sai mai zalaqa a harshen nasa ne zai iya irin wannan, don kuwa nan take aka

shirya habaicin, kuma aka yi ramuwa nan take inda ba kowa ne zai gane ba.

4.3.2 Habaici kan taimaka wajen taqaita magana:

Maganar habaici gajeriya ce sai dai mai faxin gaske, kuma cike da ma'ana idan aka warware ta. Ba a faye samun habaici da tsawo ba domin akasarin su ba sa wuce jimla xaya tak, mai yawa daga cikinsu shi ne kan kai jimla uku. Akan yi magana kaxan, amma in an zo warware ta ta xauki dogon bayani. Misali "tun ran gini ran zane". Wannan habaici taqaitacce ne amma idan aka tashi fassara shi zai xauki zance mai tsawo. Na farko dai ba abin da ya kawo maganar gini ballantana ta zane, ana magana ne a kan lokaci ko farkon da aka soma yin abu ya kamata a fidda tsarin yadda ake so wannan abu ya kasance a vangaren xan'Adam ke nan. Haka zalika idan wani abu na daxi ko na rashin daxi ya faru ga mutum, wanda bai isa ya kauce masa ba kamar na qaddara mai kyau ko mara kyau, za a iya cewa: (Tun ran gini ran zane).

Ma'ana tunda Allah (SWT) ya halicce shi ya qaddara wannan abu zai faru da shi kuma babu makawa sai ya faru. Idan muka duba za mu ga wannan jimla ce qarama amma xauke da ma'ana mai yawa.

4.3.3 Gargaxi:

Habaici yana taka muhimmiyar rawa wajen yin gargaxi ko shawara ga al'ummar Hausawa. Muna iya la'akari da kafofin watsa labarai da irin gudummawar da suke bayarwa wajen gargaxi da bada shawarwari ga al'umma ta hanyar shirya wasannin kwaikwayo da kuma gabatar da su ga jama'a. Akan yi dace wani lokaci jama'a su xauki wannan gargaxi ta hanyar wasan kwaikwayo musamman in sun ji wani abu ya yi kama da su, nan da nan sai su zaci da su ake, kuma ake wa habaici, sai su gyara halayensu domin tsarguwar da suke in sun ji an kushe su a wasanni.

Haka zalika wajen zamantakewa na jama'a in an lura wani na aikata wani abu mara kyau ana kuma tsoro ko shayin fitowa kai tsaye a gaya masa don ana tsoron sa ko kuma ana ganin girmansa. To sai a yi amfani da habaici wajen faxakar da shi ko a gargaxe shi ko kuma a ba shi shawara, in an dace kuma zai iya xauka, a nan ana iya jefa masa habaicin ne yayin da ake hira da shi kuma idan wani abu ya faru sai a fake da shi a yi masa habaici. Misalan habaici

- (Ramin mugunta gina shi gajere)

  Wannan habaici yana gargaxi ne ga wanda yake qoqarin aikata mugun abu ko yin mugunta ga wani domin ya sauqaqa ko ya bari domin abin yana iya dawo wa ko faxa wa kan sa.

- (Duniya rawar ’yanmata na gaba ya koma baya)

  Wannan habaici gargaxi ne ga wanda ya sami xaukaka ko duniya da ya bi a hankali ko kuma ya bi da waxansu ke qasansa a hankali domin wata rana yana iya yin qasa na qasansa su koma sama.

- (Don tuwon gobe ake wanke tukunya)

  Wannan habaici gargaxi ne ga jama’a, musamman ga wanda ya ke cin moriyar wani ko wani abu, da ya riqe abin nan da kyau saboda amfanin gaba.

- (Gani ga wane ya ishi wane tsoron Allah)

  Wannan habaici gargaxi ne ga jama’a da a yi hattara musamman wajen yin la’akari da abin da ya faru ga wani a kiyaye afkuwarsa a gaba.

4.3.4 Huce Takaici

Al’ummar Hausawa sukan yi amfani da habaici don huce takaici. In wani abu ya faru a tsakaninsu wanda ya sanya vacin rai a zuciyar xaya har ya zama ya qullaci abokin nasa, yakan iya amfani da habaici don huce takaici. Misalan habaici na huce takaici:

- kowa ya ci tuwo da mu, miya ya sha
- In rana ta fito, tafin hannu ba ya kare ta
- Banza a banza, Nasara ya ga zagi.
- Rabo na wajen Allah, da wajen mutum ne ba zai ba wani ba.
- In Allah ya yi maka maraba, Annabi sai ya yi maka shimfixa.

Baya ga jigogi da amfani da habaici ke da shi, ba a bar shi a baya ba wajen illoli waxanda suka haxa da tsokanar faxa da rowa da kuma hassada.

Tsokanar Faxa

Hausawa sukan yi wa junansu habaici don neman faxa. Akan xauki duk mutumin da ya cika habaici a matsayin mai neman faxa. Za mu iya danganta wannan da karin maganar da Hausawa suke cewa: “Maso habaici maso faxa, wanda ya tanka ya fi shi”.

Misalan habaici na tsokanar faxa su ne:

- Wurqilili angon kaza
- Malam dogo (gajere ko wada)
- Gurgun mage.

Waxannan habaici ana tsokana ne ga mutumin da ke da wata naqasa, sai a danganta wannan nakasar a gare shi, ko wata halitta da Allah ya yi masa.

Ire-iren wasu habaice-habaicen na tsokanar faxa sun haxa da:-

- Wa zai ba shegiya doya ubanta bai noma ba.
- A zuba wa ungulu qwan zabuwa.
- Bawa ba ya gasa da xa.

Hassada

Hassada ita ce qin wani abu na alheri ga mutum watau ganin qyashi a kan wani abu mai kyau da ya shafi rayuwa. Hausawa sukan yi wa junansu hassada a zamantakewar su ta yau da kullum. A nan za a iya zagin mutum ne

ko kuma a kushe masa duk wani abu da ya yi na rayuwa, mai kyau ko mara kyau, alhalin masu kushe masa ba za su iya yin wannan abin ba.

Don haka wannan na iya saka mutum ya yi wa masu yi masa hassada habaici kamar haka:

(Hassada ga mai rabo taki)

Haka kuma akwai habaicin da yara ne suka fi yi wa junansu amma shi ma hassada ce. Misali idan xaya daga cikin su ya yi wanka da ado, ragowar yara sai su riqa faxin:

(Ba tsari aljana a kabet), ma'ana adon da ta yi bai yi kyau ba.

Rowa:

Rowa ma wani yanayi ne da kan sa a yi habaici. Misali idan mutum yana zaune cikin mutane, sai suka nemi wani abu daga wurinsa da suke ganin yana da hali, sai shi kuma ya hana. To jin zafin haka na iya sa su kuma su yi masa habaici da cewa ai ba a kansu aka fara rowa ba ko kuma shi ba daga kan su ya fara ba. Dagan nan sai su yi masa habaici su ce:

"Mu da muka zauna da zumbuli". (Zumbuli wani mutum ne da Hausawa suka ce wai shi ne kakan marowata).

Habaici yana da wasu illoli ga al'ummar Hausawa musamman lokacin da aka yi shi. Shi habaici yi ne da mutum cikin magana a voye, ma'anar gugar zana. Akan yi shi don kawai a sa mutum ko wasu jama'a su tsargu, saboda wani abu da ake faxa. Haka kuma duk wanda aka yi wa shi to babu

shakka zai zama cikin damuwa, sannan yana nan a riqe da wanda ya yi masa har shi ma sai ya ga wani abu da zai sa ya rama ta kowacce hanya ko ta kowane hali. To ashe in haka ne kuwa za a iya samun rashin zaman lafiya da rashin jituwa in an yi habaici. Wanda hakan ba abu ne mai kyau ga al'ummar Hausawa ba domin ba ya cikin halayyarsu maikyau ta zamantakewa da suke yi a junansu.

Haka kuma habaici yakan kawo rashin jituwa ko girman kai, wanda wannan ya fi samuwa ga masu mulki, saboda shiga tsakanin su da maroqa da mawaqa suke yi don neman abin masarufi.

Illolin da akan samu in an yi habaici kan danganta da irin halin da ya sa aka yi habaicin. Duk lokacin da aka yi habaici ba a cika rabuwa lafiya ba, sai an sami wani abu ya faru, wanda zai iya zama vacin rai a fili ko ya zama na zuci wanda a nan ne ake samun qullaci, kuma shi ne masomin gaba da qiyayya.

Duk da waxannan illoli da habaici ke da su ya qunshi wasu hikimomi da sarrafa harshe, ga kuma raya al'adu da inganta su. Sannan yakan daxa kyautata harshe da bunqasa rumbunsa na kalmomi da qara masa kwarjini da martaba. Haka kuma yana saurin isar da saqo a fakaice, zuciya ta nutsu domin ta sami damar isar da burin da ke cikinta.

A kodayaushe habaici zai sa a dinga tunani a kan dukkan abin da za a aikata. A wajen mai yin habaici kuwa zai sami farin ciki da nishaxi, shi

kuma wanda aka yi wa shi zai sami damuwar da za ta zame masa hannunka mai sanda.

4.4 Kammalawa

A nan aka zo qarshen babi na huxu, a inda ya warware mana su wanene Hausawa da yadda al'adunsu suke da kuma matsayin habaici ga rayuwarsu.

Dangane da matsayin habaici kuwa, babin ya fayyace mana saqonnin da habaici ke xauke da su musamman na kushe da faxakarwa da wa'azantarwa tare da fayyace mana irin illolin da habaici ke da su, waxanda suka haxa da tsokanar faxa da rowa da hassada da makamantansu. Inda aka fi bada misalan shiryayyun karin magana da akan yi habaici da su.

BABI NA BIYAR: SALO A HABAICI

5.0 Gabatarwa

Idan aka ce salo a wannan vangare ana magana ne a kan yadda habaici yake zuwa da zavin kalmomin da ake amfani da su wajen aiwatar da shi.

Babin ya yi qoqarin nuni kan yadda ake aiwatar da habaici daidai da irin tsarin da masu aiwatar da shi ke so, domin babin ya yi tsokaci kan yadda al'ummar Hausawa ke aiwatar da shi da kuma irin salon da mata ke bi wajen aiwatar da shi kasancewar su gwanayen abin.

5.1 Ma'anar Salo da Tubalansa

Yahya (2001:2) ya bada ma'anar salo da cewa kwalliyar magana ce mai tasiri ga mai jinta.

Salo shi ke bayyana saqo, ya kuma kai shi inda aka nufa da shi. Ya qara da cewa salo dabara ce ko hanya mai yin kwalliya ga abu domin abin ya qwarzanta ko ya bayyana.

Dangane da wannan ma'ana da masanin ya bayar ya zano tubalan salo kamar haka:

i) Mallakar kalmomi
ii) Siffantawa
iii) Tsarin tunani
iv) Jaddadawa
v) Dangantakar tsari

Shi kuwa Xangambo (2007:37-40) cewa ya yi salo shi ne hanyoyi ko dabarun isar da saqo. Za a iya fassara ma'anarsa kamar haka:

i) Salo wani yanayi ne da ya qunshi zavi cikin rubutu.

ii) Salo tsari ne na daraja/armashi a cikin rubutu ko furuci.

iii) Salo ya shafi kaucewa daidaitacciyar qa'ida.

iv) Harshen wani mutum shi ne salo.

Idan muka yi la'akari da waxannan ma'anoni da masana suka bayar za mu ga cewa salo na nufin zavi cikin rubutu da ke qara wa rubutun daraja.

5.2 Salo A Habaici

Idan kuma aka ce salo a habaici ana magana ne kan yadda habaici ke zuwa tare da zavin kalmomin da ake amfani da su wajen aiwatar da shi.

Dangane da haka za mu kalli salo a habaici ta vangare biyu:

5.2.1 Salon Tsari a Habaici

5.2.2 Salon Sarrafa Harshe a Habaici

5.2.1 Salon Tsari a Habaici

A nan kuma ana duba dangantakar kalmomi a cikin habaici. Ma'ana shin habaicin wace irin jimla ya qunsa, kowace jimla na zaman kanta ne ko kuwa jimlolin sun dogara da juna don cikar ma'ana. A nan ana iya samun abubuwa a cikin wani habaicin da ba lalle ne a same su a wani ba. Dangane da haka akwai batutuwa daban-daban da za a iya gani. Musamman wajen amfani da shiryayyun karin magana don yin habaici.

5.2.1.1 Habaici mai Qaramar Jimla

Habaici mai qaramar jimla shi ne inda ake amfani da gajeriyar jimla wajen jefa habaici ta hanyar hikima da nuna gwanancewa a harshe. Ba duk mai jin harshen Hausa kan iya fahimtar tahaqiqanin wannan irin habaici ba, wani lokaci sai da bayani.

Akan yi amfani da irin wannan habaici yayin da wani abu da ya dace da shi ya zo, misalansu:

- Mugu ya san makwantar mugu
- Harara ba mari ba ce
- Gida biyu maganin gobara, da sauransu.

5.2.1.2 Habaici mai Labari

Akwai ire-iren karin magana da ake amfani da su wajen jefa habaici da kan kasance labari, wasu a yi su wasu kuma a qirqire su. Zai fi kyau a san asalin labarin kafin a fahimci habaicin. Misali:

- Ba a rabu da Bukar ba...
- Shiga uku gwauro da yaye
- Jiran gawon shanu.

5.2.1.3 Habaici mai “In ji”

Wannan kashi na habaci yana da vangare biyu, vangare na farko magana ce, na biyu kuwa sunan ko bayanin wanda ya faxi maganar.

Akan sami yanayi da ya dace da habaicin, sannan a jefa shi, akan kuma haxa vangarorin biyu da “in ji”. Misali:

- Zama wuri xaya tsautsayi, in ji kifi,
- Ashe ana tsoron iya, in ji ’ya’yan maiya
- Ala suturi buqui, in ji kishiyar mai doro
- Me na iya da abin da ya gagari wuta, in ji kishiyar qonanniya.

5.2.1.4 Habaici mai Vangare Biyu

Wannan irin habaici ya yi kama da in ji domin shi ma yana da vangare biyu, sai dai shi wannan a vangare na farko akan faxi wanda ya yi maganar, vangare na biyu kuma sai a faxi maganar tare da hali ko dalilin da ya sa ya yi maganar. Misali:

- Ni na sani, sautun mahaukaciya
- Ina sane, karuwa ta taka matar aure.
- Jiya ba yau ba, tsohuwa ta tuna tsarince
- Sabon salo, kaza ta ji ana shiqa da daddare

5.2.1.5 Habaici mai Tambaya da Amsa

Wannan kashi na habaici xauke yake da tambaya da kuma amsarta a haxe wajen gabatar da shi. Wani lokaci mai yin habaicin kan faxi vangare xaya ne ba tare da qarasawa ba. Misali:

- Me na ci na asham, balle in yi ramuwar azumi.

- Me ya fi rai na? Cin tsiren mata.

- Mu wasa ne? Bagwari ya ba da magani an mutu.

5.2.1.6 Sababbin Habaici

Idan kixa ya canza, rawa ma sai ta canza, yadda rayuwa ke sauyawa, haka ma mutane ke qago sababbin habaici da suka dace da zamani. Misali:

- Shagulatin vangaro, ungulu ta ga mushen mota.

- Banza a banza, Nasara ya ga zagi.

- Muqami, karuwa a amalanke.

5.2.2 Salon Sarrafa Harshe a Habaici

A wannan vangare za a yi bayani ne kan yadda ake amfani da harshe da kuma sarrafa shi wajen yin habaici, ma'ana yadda ake yi wa harshe ado da kwalliya wajen gudanar da habaici kai har aron kalmomi ma ba a bar shi a baya ba.

Dangane da haka za a duba abubuwa da suka haxa da:

5.2.2.1 Kamantawa

Kamantawa na nufin kamanta ko kwatanta mutum da wata dabba ko wani abu daban. Ba kuma mutum kawai ake kamantawa ba, akan xauki darajar wani abu ko halayyarsa a xora wa wani kai tsaye, ma'ana a xauki wani abu a ce shi ne kaza ko da ba a yi amfani da kalmar kamantawa ba. (Xangambo, 2007). Habaici ma ba a bar shi a baya ba domin a kan sami irin wannan kamanceceniya a ciki. Misali, "Ido ba mudu ba, ...".

An kamanta ido da mudu ne kasancewar ganin abu da ido kan bawa tunani damar ajiye wannan abu daidai da matsayinsa ko kuma ganin abu da ido kan sa mutum gane matsayi ko daraja ta wannan abu.

Wani misali na kamanci a habaici shi ne:

"Bashi hanji ne yana cikin kowa" a wannan misali an kamanta bashi da hanji kasancewar kamar yadda kowa ke da hanji a cikinsa to ba wani wanda zai ce ba ya cin bashi ko kuma ya fi qarfin ya ci bashi, don haka bashi ya zama tamkar hanji.

5.2.2.2 Abuntarwa

Abuntarwa shi ne a maida mutum, ko dabba, ko tsuntsu, ko wani abu mai rai ya zama abu marar rai kai wani lokaci ma akan xauki abu marar rai a kwatanta shi da wani abun marar rai daban, (Xangambo, 2007). Kasancewar habaici zancen hikima na Hausawa ba a bar shi a baya ba wajen abuntarwa. Misali: "mutum ba ilimi hoto".

A nan an danganta mutum da hoto wanda abu ne marar rai kasancewar bashi da ilimi kamar yadda Hausawa kan ce ilimi gishirin zaman duniya. Ma'ana a nan rayuwar marar ilimi tamkar ba ta da amfani domin in babu ilimi babu yadda za a yi a bautawa Allah (SWT) ma balle a koyi zaman duniya, sannan kuma Allah ya halicce mu ne don mu bauta masa.

5.2.2.3 Mutuntawa

Mutuntawa na nufin a xauki wata halitta marar rai a karrama ta. Akan xauki wasu halaye da siffofi ko darajoji da sauransu da mutane kawai aka sani da su, a laqaba wa wani abu marar rai ko dabba, tsuntsu, qwaro da sauransu wato wasu abubuwan da ba mutum ba, (Xangambo, 2007). Misali a xauki wata dabba ko itace a ce ta yi fushi ko ta yi magana wanda duka biyun xabi'u ne na mutane. Misali: "Ba lafiya kare ya sha taba".

Idan aka ce kare ya sha taba kowa ya san shan taba xabi'a ce ta mutum ba dabba ba don har a mutanen ma sai wanda ya ga dama ne zai sha, amma sai aka dubi kare aka ce ya sha taba wanda ba a san shi da ita ba, a nan an mutunta kare da xabi'ar xan Adam saboda hikima ta harshe cikin habaici.

Wani misali na mutuntawa a habaici shi ne: "Xan kaza na yi wa qwai dariya", sanin kowa ne cewa mutum kawai ke da ikon yin dariya ba dabba ba, balle ma a ce tsuntsu, to a nan an mutunta xankaza da cewa yana yi wa qwai dariya wanda dariya xabi'a ce ta xan'adam.

Haka kuma Hausawa kan ce “Ganin gida kare kan zagi kura”, sanin kowa ne kare da kura dabbobi ne, ba su kuma da ikon yin magana, amma sai aka mutunta kare aka ba shi ikon yin magana, har ma da yin zagi kamar yadda mutane ke yi.

5.2.2.4 Dabbantarwa

Dabbantawa na nufin bai wa mutum wani hali ko xabi’a irin ta dabba, a taqaice dai dabbantarwa na nufin mai da mutum ko wani abu dabba ko da kuwa ba shi da ikon yin xabi’u na dabbobin, kamar haushi da haniniya da sauran xabi’u na dabbobi, (Xangambo, 2007).

Akan sami irin wannan danbantawa a cikin habaici. Misali: “Xan tsako samu ka qi dangi”.

A wannan misali na habaici an yi amfani da dabbantawa inda aka maye sunan mutum da xan tsako don voye sunan wani da in ya samu abin sa ba ya iya bawa kowa sai dai ya ci shi kaxai. Haka kuma xabi’ar ‘yan tsaki take domin in sun sami abu sukan gudu ne su cinye su kaxai, sannan su dawo wurin sauran. Akan yiwa irin mutanen da ana zaune da su tun babu daxi, sai wani abun arziqi ya same su sai su gudu su bar sauran da aka sha wuyar tare irin wannan habaicin.

5.2.2.5 Rayarwa

Rayarwa na nufin xaukar wani abu marar rai, tamkar mai rai ta hanyar ba shi wani hali ko xabi'a irin na masu rai. A taqaice a xauki wata halitta marar rai kamar dutse ko gida ko riga a ba su halayya irin ta halitta mai rai a nan an rayar da su ke nan, (Xangambo, 2007). Misali: "Rijiya ta ba da ruwa guga ta hana".

Idan an duba misalin wannan habaici za a ga an rayar da rijiya da guga kasancewar ba su da rai amma aka raya su da kyauta da rowa, wanda xabi'a ce ta mutane. Akan danganta wannan habaici da mutane biyu wanda xaya zai bayar ko yin qoqarin bada wani abu sai na biyun ya hana, kasancewar yana da damar da zai yi hakan.

Haka kuma akan ce "Kar dai allura ta tono garma". A nan an rayar da allura da garma an ba su xabi'a irin ta abu mai rai. Akan yi amfani da irin wannan karin magana idan wani abu ya faru tsakanin mutum biyu inda mai laifin zai nemi wuce gona da iri in an qyale shi, to sai a nuna masa cewa ba a son fito da komai fili.

5.3 Salon Habaicin Mata

Al'ummar Hausawa kusan gaba xayansu suna yin habaici. Wato maza da mata da tsofaffi da 'yan mata da samari. A iya cewa yara ne kaxai ba su amfani da shi don ba su san inda kansu ke masu ciwo ba.

Duk da cewa al'ummar Hausawa suna amfani da habaici, kusan mata sun fi. Babu wani rukuni da aka fi sani da yin habaici kamar mata, wata qila

hakan ya faru ne saboda ba su rabuwa da ’yan ka-ce-na-ce da yawan qananan maganganu da ’yan gutsiritsoma da kuma saurin tashin hankali.

Ana samun habaici masu yawa a tsakanin kishiyoyi, ma’ana matan mutum guda suke yi, su-ya-su. Wannan yakan faru ne saboda kishi da yawan tashin hankali da ake samu a tsakanin kishiyoyi. Don haka akwai tsagwaron habaici a wannan vangare.

Habaicin mata shi ne habaici wanda da an ji shi za a san mace ce ke yi wa ‘yar’uwarta mace, kamar abokiyar zama ko maqwabciya ta hanyar fuskantar ta da take da shi musamman game da abubuwan da suka shafi su matan. Akwai kuma wanda daga ji za a san mace ce take yi wa maigida. Har ila yau akwai wanda daga ji za a san budurwa ce take yi wa saurayi ko wani namiji. Shi ma ta hanyar fuskantarsu da ta yi da shi ko dangane da yanayin zama da ke faruwa tsakanin mata da maza.

Yawancin habaicin mata karin magana ne wanda sukan yi da nufin baqantawa ko cusawa kishiya baqin-ciki. A yawancin lokutta sukan yi amfani ne da sashin farko na karin maganar, don wani lokaci ma har kwaskwarima suke yi wajen faxi. Misali – “Wai jiya ba yau ba” da “tsoro ya farar kura” da “a sayar” da “abin ba tsari” da “wa’e” da sauransu. Salon habaicin mata ya sha bamban ne, domin an fi jin irin su daga bakin matan duk kuwa da ba dole sai ga su xin kawai ba. Takan iya yiwuwa a wasu lokuttan maza su yi amfani da su. Mafi akasarin irin waxannan habaice-habaice an fi yin amfani da jinsin mata wajen gudanar da su. Sannan kuma

cike suke da adon harshe da tsohuwar Hausa tare da aron kalmomi. Ga misalin su: “Qaryar qiri ta mai ce”.

Mace kan yi wa kishiyarta wannan habaici don ta nuna mata cewa ba ta fi ta komai ba, ma’ana duk daidai suke tunda mijinsu xaya ne don haka ko da tana mata wata xagawa ta nuna ta fi ta to babu abin da ta fi ta.

“(Ina sane) karuwa ta taka matar aure”.

Mata na amfani da wannan habaici a tsakaninsu yayin da wata ta yi wa wata wani abu na ba daidai ba, sai ita kuma xayar ta yi qoqarin nuna mata cewa ta yi mata abu kaza, ita kuma sai ta nuna ai da niyya ta yi ba don ba ta sani ba.

“(Ba ki da gashin wance) ba kya yi kitson wance ba”.

Mace na iya yi wa mace ’yar’uwarta wannan habaici ne don gargaxi kan cewa kar ta kuskura ta yi gasa da wadda ba tsararta ba domin kuwa ba za ta yi kamar waccan xin ba.

“(Ba kuka na ba) uwar kishiya ta mutu”. Mace kan gudanar da wannan habaici ne yayin da ta ga wani abu wanda ba ta ra’ayinsa take kuma qoqarin ta nuna wa mutane cewa ita ba ta ra’ayin wannan abu ko kuma ba abin da ya shafe ta ba ne.

“(A gayar) bora ta yi yaji”. Mace kan yi wannan karin maganar habaici yayin da ta ga wani abu da ba shi da muhimmanci take kuma qoqarin ta nuna ita idan wannan abin ya suvuce ta ma fi jin farin ciki kasancewar ba muhimmanci yake da shi a wurinta ba.

“Mai tuya da ruwa bare ta sami mai”.

Wannan habaici yana nuni da wata ce take yin abu babu dalili ko kuma take so ta yi abu sai dalilin yin wannan abin da take jimirin yi ya samu, to ka ga ai dole ne ta yi.

“Wance tsoro ya farar kura”.

Mace kan yi amfani da wannan habaici ga ’yar’uwarta yayin da ta kasance matsoraciya, musamman ga tsaranakunta ko abokan zama, to sai a ce wance tsoro ya farar kura.

“Sauna kamar a kife ta da kwando”.

Mace kan yi amfani da wannan habaici ga ’yar’uwarta a yayin da take so ta yi mata ba’a a vangare har biyu, na farko vangaren xabi’a na biyu kuma vangaren halitta. Wato wannan mata shashasha ce ko kuma wawa ce ga ta kuma gajeriya, don ta ce kamar a kife ta da kwando.

“Ba tsari aljana a kabet”.

Wannan habaici daga ji hassada ce yara mata suke yi wa ’yar’uwarsu idan ta yi tsabta da kwalliya sai su riqa faxa mata haka da nufin yin hassada gare ta.

“Jiya ba yau ba, tsohuwa ta tuna tsarance”.

Daga jin wannan habaici an san mace ce ke yi wa ‘yar’uwarta mace da ke bayanta a shekaru take aiwatar da wani abu wanda ita zamaninta ya wuce har ya zamo ba za ta iya yi ba sai aka zolaye ta a kai. To sai ta mai da

wannan martani don nuni da cewa ita fa wannan abu ta wuce shi ko ya wuce ta.

“(Allah ya sawwaqe wahala) tsohuwa ta ga ajalinta kusa”.

Mace na iya yin wannan habaici ga ’yar’uwarta yayin da ta ga wani abu ya nufo ta gadan-gadan wanda babu makawa sai ya same ta take neman sauqinsa, duk kuwa da sai ya same ta xin.

“Allah suturi buqui, in ji kishiyar mai doro”.

Mace kan jefa wa ’yar’uwarta wannan habaici yayin da take so ta yi mata ba’a a kan wata halitta tata ko kuma wani abin da ta aikata mara kyau.

“(Aure ya tashi) wai an doki bora da qaya”.

Mace kan yi amfani da wannan habaici ga ’yar’uwarta a lokacin da ta aikata wani abu da zai warware wata yarjejeniya da suka yi ko kuma alqawari.

“Qaqa zan yi da abin da ya gagari wuta (in ji kishiyar qonanniya)”.

Mace kan yi amfani da wannan habaici a kan wata ko wani abu wanda ta yi iyakar qoqarinta don cimma sa amma abin ya ci tura, ma’ana ya fi qarfinta duk irin qoqari da ta yi ta kasa cimma nasara.

“Ranar bikin farar kaza balbela ba gayya ba ce”.

Mace kan yi amfani da wannan habaici a kan yanayi. Alal misali, idan an zo aiwatar da wani abu da yake ya shafi wani vangare ko wasu vangarori na mutum kamar ’yar’uwa ko qawaye amma abin bai shafi shi mutumin a kan kansa ba, ko ake ganin abin ba na tsaransa ko tsaranakunsa ba ne.

“(Abin da kamar wuya), gurguwa da auren nesa”

Akan yi amfani da wannan habaicin ga macen da take qoqarin xauko wa kanta wani abu da ake ganin wahala ne a gare ta ko ya fi qarfinta ba tare da ta yi tunanin hakan ba. To a nan sai a yi amfani da wannan habaicin don a nusar da ita ko a gargaxe ta.

“(Kokawa har da su wa’e!) Wasan kokuwa ba na gurguwa ba ne”.

Idan mace ta xauko wa kanta wani abu da ya fi qarfinta ko ta zaqe wa waxanda ba tsarorinta ba ko take yin wani abu da ya fi qarfin arziqinta, to za a iya jefa mata wannan habaicin don ta gane wannan abu ya fi qarfinta.

“Tafasar tukunya ba ta rage gefe”.

Mace na iya amfani da wannan habaici ga kishiyarta a yayin da mijinsu yake da wata xabi’a, misali faxa, wanda idan ya tashi ba ya barin kowa. To idan ta gama su ita da shi za ta iya yi wa kishiyarta wannan habaici don nuna mata ita ma ba ta gagari wannan faxan ba.

Idan muka duba wannan salon a habaice-habaice za mu ga kusan suna amfani da jinsin mata ne ko kuma matan sun fi yawaita amfani da su, sai dai wannan bai hana wasu mazan yin amfani da su a wani lokaci ba.

Habaici tsakanin mata ba wai ya tsaya ga kishiyoyin su ya su ba ne a’a, har maigida kansa ba a bar shi ba domin shi ma uwargida takan jefa masa habaici yayin da wani abu ya shiga tsakanin su. Idan shi ma mai gida

xan yi ne, sai ya rama, in kuma bai ga dama ba sai ya qyale ta don dama aikin mata ne.

Habaicin mata bai tsaya a kan kishiyoyinsu da mazajensu ba ne, har ma waxanda ba kishiyoyinsu ba, domin suna yi wa waxanda zaman haya ya haxa su ko a wurin biki ko suna ko kuma kowane irin taro.

Ba wai sukan jefa habaici ne a cikin magana kawai ba, sukan riqa zagin kishiyoyinsu ko maqwabtansu a turmi in suna daka ko a dutsen niqa. Mace kan xauki tavarya haka kawai ko ba za ta daka komai ba ta sa a turmi ta fara lugude tana zagin wadda take so ita ma kuma xayar da zarar ta ji sai ta xauki nata turmin ta rama ko kuma ta maida martani.

Misalin habaicin da mata kan yi a turmi yayin daka shi ne:

“Wa’e ‘yar gidan kafinta, mu ga zaninki,

Wannan ba zani ba ne jigida ne, mu ga irin shi.

Yarmutsai-ya tsohon fata, ku ga irin shi.

Kai ku ga irin ku ga irin, ku ga irin shi.

(Safara’u, 1994:24).

Ga misalin wani habaicin yayin daka:

“Durqusa ki auna mana ‘yar ganin qwafi,

Da ke ka auna mana kin ji daxi,

Amma yanzu mu ka auna maki kin ji haushi,

Bankaxaxxa ma sha inuwar rahaina,

Ba ki wanka ki ce wani ba shi wanka.

(Safara’u, 1994:25).

Da zarar wadda aka nufa da wannan habaicin ta fuskanci da ita ake sai ita ma ta xauki nata turmin ta mai da martani.

Ga kuma misalin irin habaicin da mata suke yi a dutsen niqa:

Kin ce ubaki ba ya sata,
Ke kika ce ubanki ba ya sata,
Tun daga nesa na ji ihu! Ihu!
Ubanki ya saci qashin miya.
(Safara’u, 1994:25).

Kasancewar an fi danganta habaicin da mata ya sa da zarar ka ji wannan habaicin ka san mace ce ke yi wa mace ‘yar’uwarta ko kuma take yi wa maigida ko kuma budurwa ke ma saurayi. Akan danganta irin yawancin habaici da mata ne don an fi jin irin su daga bakin matan, amma ba su kaxai ke amfani da su ba sai dai an fi amfani da jinsin mata ne wajen yin su.

Ga misalan su:

“Wata ta dafa ta sayar, wata ta dafa ta zubar”.

Wannan habaici kan iya xaukar ma'ana guda biyu ko dai kishiya ta yi wa kishiyarta idan ta fi ta iya girki. Ma'ana maigida da mutanen gida sun fi son abincinta ko kuma waxanda ake da sana'a iri xaya. Ma'ana xaya na iya yi wa xaya, idan an fi raja'a a kan kayan sayarwarta a kan na xayar. Abin nufi a nan shi ne, tana riga xayar sayar da nata kayan ko kuma xayar na yin kwantai.

Al'adar habaici ta fi yawa ga mata saboda a nan kishi yake ko ganin qyashi ko rashin jituwa da juna. Galibi mutane na xauka habaici salon mata ne, dalilinsu kuwa shi ne, mafi yawa a tsakaninsu kishi yake ga tsararrakinsu ko kishiyoyinsu ko surukansu ko mazajensu a lokacin da wani vacin rai ya shiga tsakani. Wannan xabi'a ta sa hatta mata maroqa da makaxa ma ba a bar su a baya ba wajen yin habaici a cikin waqe-waqensu.

Ga misali daga waqar Barmani Coge da aka saurara a kaset, a cikin waqar da ta yi wa laqabi da coge:

"Waxansu na ba mu kuxi,
Waxansu na zagin mu,
Ina ruwan wani da wani,
In ba rashin kunya ba,
Ana zama da varawom
Bare maroqin baki"

Daga jin wannan xiya na waqa an san mawaqiyar na mai da martani ne ta sigar habaici ga wata da ta yi mata kushe ga sana'arta ta waqa.

Haka nan kuma a cikin waqar mawaqiyar ta Allah Magani akwai inda take cewa:

"… biki na farar kaza, wa ya zo da ungulu 'yar burar uba".

A nan tana yin habaici ne ga wata da ta zo bikin da take wasan da cewa ita ba ta isa ta zo wannan wuri ba.

Haka zalika, an saurari kaset na Hauwa Mai Amada ta yi irin wannan habaicin a waqarta ta kishiya a inda take cewa:

"Mallam xauko kuxin ka mu je gabas,
Malam xauko allonka mu je gabas,
Sai ta ce ai ko Ikko ne zan bi ku,
Ashe karyar na nan maqe,
Ai kin ji ko 'yar Ali,
Wani mutum ba shi da zuciya,
Gara kare ma da shi".

Daga jin wannan waqa an san ana yi wa kishiya habaici ne inda ta danganta ta da karya don rashin zuciya ganin an ce za a gudu a bar ta amma ta kafe kan sai ta je.

5.4 Sigogin Habaici

Habaici zance ne mai qunshe da hikima kuma a baibai don yawanci ma'anarsa ita ce akasinsa. Idan za a yi wa mutum habaici a kan wani abu sai a samu zance wanda bai yi kusa da abin ba a saqala a magana. Wannan shi ne a lave da sabara a harbi barewa. Amma da yake biri ya yi kama da

mutum, sai ka ga wanda ake yi wa habaicin ya hasala har ma a nan take ya maida martani.

Habaici kuma yana da dangantaka da halin da ake ciki. Misali, idan mutane suna wani abu sai wani wanda ake ganin bai isa ya zo ba shi ma ya zo ya yi. To, ana iya xauka ya yi karambani, saboda haka xaya daga habaice-habaicen da za a iya yi masa shi ne a ce:

“Cin danqo har da su kaza”.

Ga wani misalin:

Wasu masu saida nama ne su biyu kullum sai su riqa yi wa juna habaici. Xaya daga cikinsu yana da babur xaya kuma ba ya da. Rannan sai shi xayan mai babur ya zo wurin sana’arsu, ya iso da gudu, ya ja birki qii kuma ya yi darjiya. Wannan abu fa ashe ya sosa wa xayan rai. Saboda haka sai da aka zo ciniki wajensa, da ciniki ya faxi, sai ya ce “Na sallama maka saboda kai ne”. Sai bayan mai cinikinsa ya jima da tafiya sai ya ce, “Da wani ne da ban sayar ba”. Ya xaga murya sama ya ce, “Ka san hanci bai san zaqin gishiri ba”. Af ashe shi kuma xayan mai babur ya gane cewa wannan habaicin dai da shi ake. Sai ya bari sai da aka zo ciniki sai ya ce, “Na sallama maka domin nawa ne, don kuwa mutum da gishirinsa in ya ga dama ya dafa qaho”.

Haka kuma, sau da yawa habaici kan gudana cikin yanayi na farin ciki. Misali idan akwai abokan gaba guda biyu a tare a wuri xaya waxanda ake tsammani wani abu mai muni zai sami xaya daga cikinsu a sakamakon

wata rawa da ya taka ba daidai ba wanda zai iya zama cikin kuskure. To wannan abu misali sai ya haifar da sakamako na akasi, wato maimakon mummunan sakamako sai ya bada kyakkyawa. To za mu ga a lokacin da wannan abu ya faru shi wanda ake tsammanin mugun abu zai same shi zai yi farin ciki qwarai, kuma idan da hali zai yi yunqurin maida martani ta hanyar habaici wanda zai nuna yanayin farin cikinsa da kuma maganganu na cusa haushi ga abokan adawa. Misali

- Zakaran da Allah ya nufa da cara, ko ana muzuru ana shaho sai ya yi.
- Ciki da gaskiya wuqa ba ta huda shi.
- Gyaxar Dogo, sama ‘ya’ya qasa ‘ya’ya.
- In ba ki ya zama daidai, hannu ba ya zama daidai.

Idan muka duba za mu ga duk irin waxannan misalai na habaici da aka kawo suna komawa ne zuwa ga yanayi na farin ciki da wani ya shiga har ya kai shi ga kare kansa ko kwarzanta kansa ta hanyar waxannan habaici.

Haka kuma kamar yadda habaici ka iya zamowa ta hanyar farin ciki yakan kuma iya canza zane ya zamo ta hanyar baqin ciki domin wani abu har ila yau habaici yakan faru har ya yi sanadiyyar sakawa shi mai faxin habaicin vacin rai. Sau da yawa a kan ji Hausawa suna faxin cewa:

“Allah wadaran naka ya lalace, wai da raqumin dawa ya ga na gida.

Ko kuma su ce: “Ba haka aka so ba qanin miji ya fi miji kyau”.

Idan suka yi nazari da kyau za a ga duk waxannan misalai guda biyu da aka ambata an gudanar da su ta hanyar vacin rai da aka haifar wa mai yin su.

Haka nan idan aka duba habaice-habaice kamar “Banza girman qashi ba tsoka”. Ko da wata sigar a ce “Banza girman mahaukaci qaramin mai wayo ya fi shi”.

Dukkan su za a ga hanya ce da aka bi don bayyana baqin ciki ta yin habaici, domin kuwa za mu ga cewa shi wannan habaici da aka yi wa wata ko wani yana nuna gazawar su ne ga abin da aka yi tsammani za su aikata, sai su aikata qasan haka, domin kuwa ita kalmar girma da aka ambata tana nuni ne ga alamar muqami ko daraja amma kasancewar in girman a hauka ne sai ya zama na banza, sai aka kawo kalmar qarami ya zauna a muhallin girma wajen bada abin da aka buqata, wanda ba siffar sa ba ce tun asali na girman ne, amma sai ta sami cancanta a sakamakon haxa ta da wayo wanda shi ne abin da ake so a samu a wurin mahaukaci, amma ba a samu ba. Duk wanda aka yava wa maganar ba mahaukaci ba ne to amma kasancewar da ma can maganar a habaice ake yin ta to sai aka ari kalmar mahaukaci ta maye gurbin wanda ba a sami abin da aka nema ko ya dace daga wurinsa ba.

Haka nan ma idan muka yi waiwayen baya kaxan ga misalan da aka bayar: “Allah ya wadaran naka ya lalace, wai da raqumin dawa ya ga na gida”. Ko kuma “Ba haka aka so ba, qanin miji ya fi miji kyau”.

Za a ga ba su da wani bambanci tsakanin su da wannan sharhin da ya gabata, illa dai ya danganta da abin da ya faru har aka faxi hakan don kuwa za mu iya ganin da “Alla wadaran naka ya lalace” da “Banza girman mahaukaci” duk suna nuni ne ga abin takaici da ya faru amma shi “ba haka aka so ba qanin miji ya fi miji kyau” zai iya karvar wata manufa daban. Misali idan mutane biyu ba sa jituwa sai wani ya yi yunqurin samun wata buqata to zai iya zama ko ta wace hanya buqatar sai abu ya faskara ko a 'sami cikas to xaya abokin hamayyar zai iya goranta wa xan’uwansa da cewa ba haka aka so ba.

Kamar yadda akan yi habaici a yanayin farin ciki ko baqin ciki ko kuma mu ce daxi da rashinsa akan kuma yi habaici a yanayi na nishaxi. Alal misali, mace kan yi wanka da kwalliya bayan ta tsabtace muhallinta a gidan mijinta idan tana cike da nishaxi sai kawai ta saki habaici, wannan nishaxi ko yanayi da take ciki na iya haifar mata da cewa ita ta isa ko ta kai wani muqami, daga cikinsu tana iya zama ta fi kishiyarta kyau ko tsabta ko kwalliya ko iya abinci ko matsayi a wurin mai gida da sauransu.

A nan tana iya cewa “Allah nawa, Annabi na uwata”.

5.5 Kammalawa

Wannan babi ya yi sharhi ne game da salon da habaici ke xauka na bai xaya tare kuma da fayyace irin salon da mata ke amfani da shi wajen gudanar da habaicinsu.

Binciken bai tsaya a nan ba, sai da ya fidda siga ko tsari da yanayi dukkansu na gudanar da habaici.

Wannan ya samu ne dangane da cewa kowane al'amari ko qirqira ta harshe akwai tsarin da ake bi wajen gudanar da su, haka ma yake a habaici.

BABI NA SHIDA: NAXEWA

6.0 Gabatarwa

Wannan aiki ya yi nasarar gudanar da nazarin habaici a cikin zantuttukan hikima na Hausawa, wanda vangare ne na adabin baka, qarqashin adabin gargajiya na Hausawa.

Hausawa al'umma ce da ke da zantuttukan hikima da kuma qirqire-qirqire na harshe wanda ke da mu'amalarsu ta yau da kullum a junansu. Kasancewar akan sami kishi ko rashin jituwa wani lokaci a tsakaninsu ya haifar da habaici don cimma wasu buri na rayuwarsu.

Binciken ya yi nazarin habaici ne a cikin guntattakin zantuttukan hikima na Hausawa a inda ya fayyace saqonninsa tare da irin yadda mata ke amfani da shi duk da cewa bai yi qasa a gwiwa ba wajen bayyana cewa mazan ma ba a bar su a baya ba wajen amfani da shi.

Daga nan kuma sai aka shiga cikin aiki sosai wajen bayyana muhallan da habaici ke fitowa da suka haxa da karin magana da zambo da makamantansu tare da salonsa da siga da kuma yanayin da ake gudanar da shi. Binciken ya tabbatar da cewa kasancewar habaici abu ne mai matuqar mihimmanci ya sa Hausawa ke cimma wani buri na rayuwarsu ta hanyar amfani da shi.

Kamar yadda binciken ya bayyana muhimmancin habaici ya shafi vangarori da dama na al'umma wanda hakan ya sanya amfani da shi a vangarori daban-daban.

Binciken bai yi qasa a gwiwa ba sai da ya sami damar fito da wani abu muhimmi wanda ya bambanta shi da sauran bincike masu kama da shi, domin ya nuna qarara cewa habaici na taka muhimmiyar rawa wajen wa'azantarwa da faxakarwa ta vangaren addini, wanda wannan abu ne sabo dangane da irin wannan nazarin.

6.1 Abubuwan da Bincike ya Gano

Bincike ya gano cewa baya ga ximbin amfani da mata da sauran al'umma ke yi da habaici ta fuskar baqantawa ko musgunawa an gano cewa habaici na taka muhimmiyar rawa wajen faxakarwa da ilmintarwa da wa'azantarwa ta fuskar addini da halin rayuwa na yau da kullum dangane da ci gaban addini da ilimi da kuma wayewar kai da mata Hausawa ke daxa samu.

6.2 Shawarwari

Dangane da binciken da aka gabatar a wannan fanni akwai shawarwari da ake ganin ya kamata a bi wajen farfaxo da al'adunmu, musamman na vangaren zantuttukanmu na hikima.

Sau da yawa matasa sukan yi amfani da karin magana ko habaici na zamani maimakon waxanda muke da su tun fil azal, to kasancewar haka

yake da kyau a fiddo da ire-iren hikimomi na harshen da ake da su don amfanin yaranmu wanda rashin yin hakan yana iya sakawa su vace vat, ya zama kamar ba a yi su ba.

Zai yi kyau mu nuna wa yaranmu naka shi ne naka, ma'ana mutum ya riqe harshe da al'adarsa fiye da yadda zai ari na wani domin Hausawa na cewa "kayan aro abin banza ne".

Yana da kyau kada a gajiya wajen baiwa matasa shawarwari a kan yadda za su riqe al'adunsu domin tun ba sa ganewa har za su zo su fahimci wannan abin da ake gaya musu yana da muhimmanci a gare su har ma da na baya da su.

Dangane da sha'anin rubuce-rubuce, zai yi kyau a qara qaimi wajen yin su domin rubuta abu a ajiye yana hana vacewar sa. Haqiqa rubutu muhimmiyar hanya ce ta adana tarihi, wanda shi ne yake sa ilimi ya sadu tsakanin mai rai da mara rai, ma'ana mutum kan yi nazari ko bincikensa ya samar da wani ilimi ya kuma rasu ya bar shi har wanda bai san shi ba ya gani ya kuma amfana da wannan ilimin.

A qarshe zai yi kyau manya da kansu su guje wa aron baqin al'adu na wasu vangarori daban-daban, musamman wajen nazari na makarantu.

6.3 Kammalawa

Wannan bincike da aka gabatar ya taqaita ne a cikin guntattakin zantuttukan hikima na Hausawa, wanda a cikin guntattakin zantuttukan hikiman ma an nazarci habaici ne.

A vangaren habaicin an kalle shi da idon basira, sannan aka warware saqonninsa tare da salon da yake zuwa da shi.

Kasancewar mata su ne gwanayen habaici, sai binciken ya faxaxa wajen matsayin habaicin a gurinsu tare da irin salon habaicinsu.

MANAZARTA

Azima, M. A. (2007). "*Hausa Women in the Diaspora*". Wazobia Vol. 4, No. 1, FCE, Kano.

Bargery, G.P. (1993) *A Hausa – English Dictionary and English – Hausa Vocabulary.* London: Oxford University Press. 2nd Edition.

Bichi, A. Y. (1995) "Hausa Folkgenres", cikin Harsunan Nijeriya. Vol. XVII C.S.N.L., Jami'ar Bayero Kano

Bichi, A. Y. (1997) "Current Trends and Issues in Hausa Proverbs" cikin Harsunan Nijeriya. VOL XVIII CSNL, Sashe Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero Kano

Binta, J.W. (1998) "Adabin Baka da Sigoginsu da Hikimominsu". Kundin Digiri na Biyu, Sashe Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero Kano.

Xangambo, A. (2007) *Xaurayar Gadon Fexe Waqa.* Amana Publishers, Zaria.

Xangambo, A. (1984) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*: Maxaba'ar Triumph.

Xantanko, A. S. (1977) "Harshe Tubalin Ginin Al'ada: Nazarin Hikimomin Sarrafa Harshen Hausa". Kundin Digiri na Xaya, Jami'ar Bayero Kano.

Xiso, A. H. (2009). *Tsokaci a kan Rubutattun Waqoqin Hausa*. Annuri Printing Press, Kano.

Dunfawa, A. A. (2005). "Zambo da Habaici a cikin Rubutattun Waqoqin Addini". *Journal of Hausa Studies,* Vol. 1, No. 2, Sashe Harsunan Nijeriya, Usman Danfodio University, Sokoto.

Graham F. (1996) Poetry, *Prose and Popular Culture in Hausa*. Edinburg University Press for International African Institute, London.

Gusau, S. M. (1980) Salihu Jankixi da Waqoqinsa. Qungiyar Hausa, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero Kano.

Gusau, S. M. (1988) "Waqoqin Makaxan Fada: Sigoginsu da Yanayinsu, musamman a Qasar Sakkwato". Juzu'i na Xaya, Nazari da Sharhi. Kundin Digiri Na Biyu.

Ibrahim, M. S. (1982). “Dangantakar Al’ada da Addini: Tasirin Musulunci kan Rayuwar Hausawa”. Kundin Digiri na Biyu, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano.

Ibrahim, M. S. (1983) Kowa ya Sha Kixa. Longman Publishing Co. Ltd.

Ibrahim, S. S. (1995). “Dangantakar Waqar Baka da Rubutatta ta Fuskar Zambo da Habaici”. Kundin Digiri na Xaya, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Usman Xanfodio, Sakkwato.

Magaji, A. (1980) “Nazari a Kan Rayuwa da Waqoqin Alhaji Kassu Zurmi”. Kundin Digiri na Farko, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Ahmadu Bello Zariya.

Mahuta, G. A. “*The Status of Women in Hausa Proverbs*” Studies in Hausa Language, Literature and Culture, the 5th Hausa International Conference, C.S.N.L., Jami’ar Bayero Kano

Maqarfi, S. (1970) *Jatau na Kyallu*. NNPC Zariya. Gaskiya Cooperation Ltd. Zariya.

Rabi, G. (1998) “Nazarin Jinsi a Adabi: Tsokaci kan Matsayin Mace a Rubutun Wasannin Kwaikwayo na Hausa”. Kundin Digiri na Biyu, Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya.

Rattray, R. S. (1913) *Hausa Folklore, Customs and Proverbs*. *Vol II, With Preface* by R. R. Marett: London 1913.

Safara’u, M. (1994). “Habaici da Matsayinsa ga Al’ummar Hausawa”. Kundin Digiri na Farko, Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya.

Sanyinnan, M. (2002) *Waqoqin Alhaji Mamman Shata Diwani na xaya*, Hukumar Binciken Tarihi da Kyautata Al’adu ta Jihar Katsina. Government Printing Press, Katsina.

Sanyinna, A. D. (2001). Yabo da Zambo da Habaici a Waqoqin Musa Xanba’u Gidan Buwai. Kundin Digiri na Farko, Sashen Harsuna da Al’adun Afirka Jami’ar Ahmad Bello da ke Zariya.

Umar, A. (1986) “Guntattakin Zantuttukan Hikima na Hausa”. Kundin Digiri na Farko, Sashen Harsuna da Al’adun Afirka Jami’ar Ahmadu Bello Zariya.

Umar, J. T. da wasu (1995) *Jiki Magayi*: NNPC Ltd. Zariya.

Umar, M. B. (1980) *Adabin Baka don Makarantu*. Mangwaron Babajo Zariya.

Waya, T. M. (1990) Habaici, Zambo da Karin Magana: Matsayinsu da Tasirinsu a Cikin Al'adar Hausawa. Kundin Digiri na Farko, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Yahya, A. B. (2001). *Salo Asirin Waqa*. Fisbas Media, Kaduna.

'Yar'aduwa, T. M. da wasu (2007) *Harshe da Adabin Hausa a Kammale*. Spectrum Books Ltd. Nazareth press Ltd. Ibadan.

Zarruq, R. M. da wasu (1981) *Kirarin Duniya 222*: Ganuwa Publishers Ltd. Zariya.

Zarruq, R. M. da Wasu (1986). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa*. ABU: University Press.